# Fahimtar Ko Wa Yesu Yake: Asalin Bambanci Tsakanin Musulmi da Kirista



GUÐRÚN MARGRÉT PÁLSDÓTTIR

# Fahimtar Ko Wane ne Yesu:

Asalin Bambanci Tsakanin Musulmi da Kirista

# Fahimtar Ko Wane ne Yesu:

Asalin Bambanci Tsakanin Musulmi da Kirista

GUÐRÚN MARGRÉT PÁLSDÓTTIR

Take cikin asilin harshe: The Understanding of Who Jesus Is: The Basic Difference Between Muslims and Christians
Hausa translation - Fassarar Hausa

© Mallakar 2021 – Guðrún Margrét Pálsdóttir
Mai Fassara: Rev. Wanson Yusufu Bagu
Zayyana Murfi: Karousel ehf – María Ericsdóttir Panduro
Wallafa: Wallafawar WJI
Mai Bugawa: Leturprent (2022) Reykjavík, Islanda

Za a iya buga da kuma juya wannan littafi zuwa harsuna dabam-dabam domin a yi aiki da shi banda riɓa amma tare da rubutaccen izinin marubucin ta wurin aderishi: understanding@whojesus.is
Don Allah, ka karanta da farin ciki, ka raba ka kuma cire kofi a kyauta ta wurin ziyartar yanar gizonmu: whoJesus.is

Sai dai idan an lura, in ba haka ba:
Dauko aya daga Alkur'ani duk daga:
quran-for-all.com
Version 4 (2022)

Dukan ɗauko na Littafi, sai dai idan an nuna, in ba haka ba, an ɗauka ne daga Littafi Mai Tsarki, Juyi ta Biyu © 2010, Al'ummar Littafi Mai Tsarki ta Nijeriya. Bugu na Al'ummar Littafi Mai Tsarki na Koriya.

Rubutun siffar tafiyar tsutsa, duk da nassossin Alkur'ani da Littafi Mai Tsarki, duk nanatawar marubucin ne.
Domin Rarraba a Dukan Duniya
Asalin Bugawa a Islanda

ISBN 978-9935-526-10-6 (Siffan bugu)
ISBN 978-9935-526-11-3 (Tsarin Saukuwar Takarda)

# Kallafarwa

*Ina so in kallafad da wannan takarda zuwa*
*ga ´yan´uwana na Musulmai a Iceland*

*da*

*Ga dukan waɗanda a faɗin*
*duniya suna marmarin Gaskiya.*

# Jerin Darussa


Gabatarwar Marubuci....................................................................9

Gabatarwa ..............................................................................11

Babi na 1: Yesu Bisa ga Ra'ayoyi Dabam-Dabam ...............................13

Babi na 2: Yesu ya Mutu a Bisan Gicciye?...........................................21

Babi na 3: Yesu Shi Ne Ɗan Allah?........................................................ 33

Babi ta 4: Yesu da Kansa Allah ne? ....................................................39

Babi na 5: Yesu Shi Ne Mai Ceton Duniya? ........................................47

Babi na 6: Yesu Shi ne Matsakanci Tsakanin Allah da 'Yan Adam? ..51

Babi na 7: Tabbaci na Tushen Rubutu .................................................55

Rufewa: ..................................................................................63

Sunayen Yesu a Cikin Alkur'ani da kuma Littafi Mai Tsarki .............64

Kima na Koyarwar Yesu: ...................................................................65

Takardun Shaida: ...........................................................................67

# Gabatarwar Marubuci

Ba tare da rashin tunani a yi zaton cewa mafi yawan masu karanta wannan takarda su ɗauki kansu sun san wa Yesu yake ba. Wannan zai iya zama saboda abin da sun karanta a cikin Alkur'ani ko a cikin Littafi Mai Tsarki, ko kawai sakamakon abin da sun ji ko kuwa an koyar da su a ɗa.

Wannan takarda ta yarda wa masu karatu su yi tunani a gefe dabam-dabam. Idan mutum ya san gefe ɗaya kawai, zai yi wuya ya ga babban hoton. Yana ɗaukan karfin hali a dubi gefen da mai yiwuwa ba ka da cikakken fahimi ba tukuna. Ta yin haka, abin da ka gaskata shi ne gaskiya zai iya tabbatu ko kuwa a kalubance ka ga ƙarin bincike domin ka gina rayuwarka a kan gaskiya.

Da gaske ina kauna da kuma mutunta Musulmi, Kirista da Yahudawa, da kuma mutanen wadansu adinai. Duk da haka, fiye da kome kuma, ina kaunar gaske. Wato ginshiki wadda ina so in gina rayuwata. A wannan haske, na yi nazarin Littafi Mai Tsarki da Alkur'ani duka. Ta wurin rubuta wannan takarda, ina so in raba wadansu muhimman batutuwa da an rubuta game da Yesu a cikin wadannan littatafi na kwarai.

Addu'a ta shi ne za ka karanta wannan takarda da zuciya a bude, a shirye ka bincika gaskiyar wane ne Yesu da gaske.

*Guðrún Margrét Pálsdóttir (Gunna Magga)*

# Gabatarwa

Yahudawa, Kirista da Musulmi duka sun gaskata da Allah ɗaya sun kuma gina a tushe iri ɗaya, labaran mutane masu bangaskiya kwarai kamar su Ibrahim, Musa da wadansu annabawa na Littatafai.

Kirista sun gina akan Littafi Mai Tsarki ɗaya kamar Yahudawa, wanda ake kira Tsohon Alkawari da kuma karin Sabon Alkawari wanda ya yi fadi game da zuwan Yesu Almasihu (Masiha), rayuwarsa da kuma ikkilisiya ta farko.

Musulmi sun gina akan Alkur'ani wadda yake fadi game da mutane da yawa iri na Littafi Mai Tsarki, amma da ɗan bambanci kaɗan.

Alkur'ani yana magana game da Littafi/Nassi (Littafi Mai Tsarki), mutanen Littafi/Nassi (Yahudawa da Kirista) da kuma Yesu a matsayin Almasihu (Masiha)/Kristi.

Littafi Mai Tsarki ya kunshi annabce-annabce fiye da 300 game da Almasihu (Masiha) a cikin Tsohon Alkawari, kuma a cikin Sabon Alkawari akwai cikakken labarai na rayuwar Yesu da shaiɗu suka rubuta wadda take nuna cikawar dukan wadancan annabce-annabcen cikin Yesu.

Bugu da kari, wadansu masu ilmin tarihi da marubuta na karni na fari da na biyu sun ambaci Yesu a cikin rubutunsu da kuma abubuwa da sun faru waɗanda suke daidai da bayyanin Littafi Mai Tsarki.

Kirista da Musulmi sun yarda cewa Yesu ne Almasihu (Masiha), sa'ad da yawancin Yahudawa ba su gaskata da Yesu ba kuma har yanzu suna jiran zuwan Almasihu (Masiha).

Ko da shike Yesu da kansa da almajiransa na fari duka Yahudawa ne, shugabannin Yahudawa suka ki shi, masu mulkin addini kuma suka tuhume shi suka kashe shi akan ya yi sabo. Ko da shike yau, Yahudawa da yawa suna kan gane cewa Yesu hakika Almasihu (Masiha) ne da aka alkwarta.

A cikin wannan takarda zan yi ƙoƙarin fadakar da ganewar Yesu domin in bayyana gaskiya game da shi, wanda Musulmi suke mutunta sosai kuma Kirista suke ƙauna da kuma yi masa sujada.

*Babi Na 1*

# Yesu Bisa Ga Ra'ayoyi Dabam-Dabam

**Littafi Mai Tsarki da Alkur'ani sun Yarda akan Wadannan:**
Ɗa Yesu ne Almasihu (Masiha), annabi ne kuma, kalmar gaskiya, kalmar Allah. Ya iya warkar the marasa lafiya, ya ba da gani wa makafi da kuma ta da matattu/ba da rai. Mala'iku sun sanar da zuwansa a cikin wannan duniya, budurwa ce ta haife shi, saboda haka haifuwarsa na allahntaka ne, ta tsakanin Allah. Ya hau cikin sama, yana da rai yau kuma zai dawo.

**Alkur'ani** ya fada da cewa Yesu shi ne Almasihu (Masiha) amma bai bayyana cikakke hakkin Almasihu (Masiha) bisa ga annabce-annabcen da ba. Lokacin da ake bukata bayyani ko kuwa kamar yadda aka furta a *Alkur'ani 10:94* da *16:43*, idan mutane ba su sani ba ko kuwa suna cikin shakka, an shawarce su da su nemi amsoshi a cikin Littafi/Nassi (Littafi Mai Tsarki) ko kuwa su tambayi waɗanda suka karanta shi.

Saboda haka, bari mu dubi wadansu annabce-annabcen Tsohon Alkawari a cikin Littafi game da Almasihu (Masiha), dauke da bayyanin haifuwarsa, aikinsa da mutuwarsa. Dukan waɗancan tsofin annabce-annabcen suka cika cikin Yesu kamar yadda aka bayyana shi a wadannan kwatanci.
Za a sami wadannan cikawar duka a cikin Linjila (Bishara) na Sabon Alkawari da kuma waɗansu a cikin Alkur'ani.

**Annabce-Annabce da Cikawarsu:**

Haifuwar Yesu – Za a Haife Shi ta wurin Budurwa
**Annabci:** *Ishaya 7:14; Ishaya 9:1-7*
**Cikawa:** *Matiyu 1:18-25; Luka 1:26-38; Alkur'ani 19:19-22*
Wurin Haifuwarsa – Za a Haife Shi a Baitalami
**Annabci:** *Mika 5:2*
**Cikawa:** *Matiyu 2:1-11; Luka 2:1-7*
Zai kawo gafartawa da sabuntawa; warkarwa da ganin gari ga makafi
**Annabci:** *Ishaya 42:6-7; 61:1-3; Zakariya 13:1*
**Cikawa:** *Markus 2:1-12, 17; Luka 4:14-21; 6:19; 7:21-22; 11:5-6; 18:35-43; Alkur'ani 3:49*
Zai Zama Kwatancin Tawali'u – Sarki a bisan aholaki.
**Annabci:** *Zakariya 9:9*
**Cikawa:** *Matiyu 27:37; Markus 11:7-10*
Za a bashe Shi a kan tsabar azurfa 30
**Annabci:** *Zabura 41:9-10; Zakariya 11:12-13*
**Cikawa:** *Matiyu 26:14-15; 27:3-10*
Za a yi Masa duka, a yi masa ba'a, a kuma tofa masa yau
**Annabci:** *Ishaya 50:6*
**Cikawa:** *Matiyu 26:67; 27:26; Markus 14:65*
Za a gicciye Shi
**Annabci:** *Zabura 22:1-19*
**Cikawa:** *Matiyu 27:22-44; Markus 15:16-41; Luka 23:22-49; Yahaya 19:1-37*
Zai mutu domin zunubanmu
**Annabci:** *Ishaya 53:4-12*
**Cikawa:** *Matiyu 26:28; 1 Bitrus 2:24*
Rana za ta dauke haske kuma duhu za ta kasance daga tsakar rana a ranar da ya mutu
**Annabci:** *Amos 8:9-10*
**Cikawa:** *Matiyu 27:45; Markus 15:33; Luka 23:44*
Zai zama hasken duniya
**Annabci:** *Ishaya 9:2, 6; 60:1-3*
**Cikawa:** *Yahaya 1:4, 9; 12:46*

**Abin da Yesu ya ce game da kansa, yadda kuma almajiri Yahaya ya rubuta:**

*"Ni ne gurasa mai ba da rai. Wanda ya zo gare ne ba zai ji yunwa ba har abada, wanda kuma ya gaskata da ni ba zai kara jin kishirwa ba har abada." (Yahaya 6:35)*

*"Ni ne hasken duniya. Wanda yake bi na ba zai yi tafiya a duhu ba, amma zai sami hasken rai." (Yahaya 8:12)*

*"Ni ne kofar. Kowa ya shiga ta wurina zai sami ceto…" (Yahaya 10:9)*

*"Ai, ni ne tashin matattu, ni ne kuma rai. Wanda ya gaskata da ni, ko ya mutu zai rayu." (Yahaya 11:25)*

*"Ni ne hanya, ni ne gaskiya, nine kuma rai." (Yahaya 14:6)*

*"Ni ne makiyayi mai kyau. Makiyayi mai kyau kuwa shi ne mai ba da ransa domin tumakin." (Yahaya 10:11)*

*"Ni ne tsatson Dawuda, da zuriyarsa, Gamzaki mai haske." (Wahayin Yahaya 22:16)*

*"Ni ne Alfa, Ni ne Omega, Ni ne na Farko, Ni ne na Ƙarshe."*
*(Wahayin Yahaya 22:13)*

*"Ku daga kasa kuke, ni kuma daga sama nake. Ku na duniyan nan ne, ni kuwa ba na duniyar nan ba ne." (Yahaya 8:23)*

*"In dai kun zauna kan maganata, hakika ku almajiraina ne. Za ku san gaskiya, gaskiyar kuwa za ta 'yanta ku." (Yahaya 8:31-32)*

*"Wannan fa shi ne umarnina, cewa ku kaunaci juna kamar yadda na kaunace ku. Ba kaunar da ta fi haka ga mutane, wato mutum ya ba da ransa saboda aminansa." (Yahaya 15:12-13)*

**Taburin Ra'ayoyi Dabam-Dabam akan Wa Yesu Yake**

| **YESU** | **Almasihu a Tsohon Alkawari** | **Yesu a Sabon Alkawari** | **Yesu a cikin Alkur'ani** | **Tabbacin Masu Ilmin Tarihi** |
|---|---|---|---|---|
| **Haifuwar Budurwa** | I *Ishaya 7:14* | I *Matiyu 1:18-23; Luka 1:26-38* | I *Alkur'ani 19:19-22* | |
| **Annabi** | I *M./Shari'a 18:18; 34:10-12* | I *A. M. 3:20-22; Matiyu 13:57; 21:11* | I *Alkur'ani 19:30* | I *Lucian 1)* |
| **Kalmar Allah** | | I *Yahaya 1:1-14* | I *Alkur'ani 3:45* | |
| **Kalmar Gaskiya/ Gaskiya** | | I *Yahaya 14:6* | I *Alkur'ani 19:34* | |
| **Hasken duniya** | I *Ishaya 9:2; 60:1-3* | I *Yahaya 1:4, 9; 12:46* | | |
| **Warkar da Marasa Lafiya** | I *Ishaya 61:1; 53:5* | I *Luka 8:43-48; Matiyu 9:35; 21:14* | I *Alkur'ani 3:49* | |

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| **Ba da Ganin Gari wa Makafi** | I *Ishaya 42:6-7* | I *Luka 7:21-22* | I *Alkur'ani 3:49* | |
| **Tā da Matattu/ Ba da Rai** | | I *Luka 8:49-55* | I *Alkur'ani 3:49* | |
| **Ya yi Al'ajibai** | I *Ishaya 35:4-6* | I *Markus 7:32-37* | I *Alkur'ani 3:39* | I *Talmud na Babila 2) Josephus 3)* |
| **Ɗan Allah** | I *Zabura 2:7, 12* | I *Yahaya 3:16; 1 Yahaya 1:3* | I *Alkur'ani 19:88-92* | An yi masa Sujada bayan tashinsa daga matattu: *Pliny the Young 4), Lucian* |
| **Masiha/ Kristi** | I *Ishaya 9:1-7; 61:1-3* | I *Matiyu 2:1-5* | I *Alkur'ani 3:45* | I *Tacitus 5), Pliny the Younger, Josephus* |
| **Mai Ceto** | I *Ishaya 35:4-6* | I *Luka 2:10-11; Matiyu 20:28* | A'a *Alkur'ani 3:84* | |

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| **Gafarta Zunubai** | I<br>*Ishaya 1:18; 53:3-12* | I<br>*Markus 2:5-12; Matiyu 1:21* | A'a<br>*Alkur'ani 5:75* | |
| **Matsakanci Tsakanin Allah da 'Yan Adam** | I<br>*Ishaya 42:6* | I<br>*1 Timoti 2:5* | A'a<br>*Alkur'ani 2:255* | |
| **Shi Allah ne** | I<br>*Ishaya 9:6-7; 35:4-5* | I<br>*Yahaya 1:1; 20:28-29* | A'a<br>*Alkur'ani 5:72* | |
| **An yi Masa Baftisma** | | I<br>*Matiyu 3:13-17* | | I<br>Yarjejeniyar yawancin masana a yau |
| **An Gicciye Shi** | I<br>*Zabura 22:2-19* | I<br>*Matiyu 27:32-50; Markus 15:1-37; Luka 23:13-46; Yahaya 19:1-30* | A'a<br>*Alkur'ani 4:157* | I<br>Yarjejeniyar yawancin masana a yau; <u>Tsohon tushe;</u> *Lucian, Tacitus, Josephus, Talmud na Babila* |

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| **An Binne Shi a Kabari** | I<br>*Ishaya 53:9* | I<br>*Matiyu 27:57-66* | | I<br>Masu Ilmin Tarihi gaba ɗaya sun yarda |
| **Ya Tashi daga Matattu** | I<br>*Ishaya 53:10; Zabura 16:10; 49:16* | I<br>*Matiyu 28:1-15; Markus; 16:1-7 Luka 24:1-7; Yahaya 20:1-18; A. M. 2:22-27* | I<br>*Alkur'ani 19:33* | I<br>Makasudin masana da yawa a yau. Tsohon tushe; *Josephus, Tacitus* |
| **Ya Hau cikin Sama** | I<br>*Zabura 68:18; Daniyel 7:13-14* | I<br>*A. M. 1:9* | I<br>*Alkur'ani 3:55; 4:158* | |
| **A Raye yake yau** | I<br>*Ishaya 9:6-7* | I<br>*Matiyu 28:18-20; Wah. Yah. 1:12-18* | I<br>*Alkur'ani 4:158* | |
| **Zai Dawo** | I<br>*Daniyel 7:13-14* | I<br>*Yahaya 14:2-3; A. M. 1:9-11; Wah. Yah. 1:7* | I<br>*Alkur'ani 4:149 43:61* | |

**Za a iya kunsa babban bambanci na ganewar Yesu tsakanin Musulmi da Kirista a cikin waɗannan tambayoyi:**

Yesu ya mutu a bisa gicciye?
Yesu shi ne Ɗan Allah?
Yesu da kansa Allah?
Yesu ne mai ceton duniya?
Yesu ne matsakanci tsakanin Allah da ‘Yan Adam?

A cikin Alkur’ani amsa shi ne babu ga duka wadancan tambayoyi amma a cikin Littafi Mai Tsarki amsa shi ne I ga dukansu.

Bari mu lura sosai ga kowane tambaya da kuma yadda amsoshin sun bambanta a cikin Alkur’ani daga wadancan a Littafi Mai Tsarki.

*Babi Na 2*

# Yesu Ya Mutu A Bisa Gicciye?

**Alkur'ani yana koyar cewa ba a gicciye Yesu ba:**
*Da faɗarsu: "Lalle ne mu, mun kashe Masĩhu Ĩsã ɗan Maryama Manzon Allah," alhãli kuwa ba su kashe shi ba, kuma ba su kẽre shi ba, kuma ammaan kamanta shi ne a garẽ su. Lalle ne waɗanda sauka sãɓã wa jũna a cikin sha'aninsa lalle ne, sunã shakka daga gare, shi, bã da wani ilmi fãce bin zato kuma ba su kashe shi ba bisa ga yaƙĩni. Ã'a, Allah Ya ɗauke shi zuwa garẽ Shi, kuma Allah Yã kasance Mabuwãyi, Mai hikima.(Alkur'ani 4:157-158)*

Duk da haka, a wasu wurare, Alkur'ani ya nuna cewa Yesu ya mutu kuma a bayan wannan ya tashi daga matattu. Bisa ga Alkur'ani Yesu ya yi magana sa'ad da yake kwana biyu da haihuwa, yana nuna cewa zai mutu:

*"Kuma Yã sanya ni mai albarka a inda duk na kasance kuma Ya umurce ni da yin salla da zakka matuƙar inã da rai." "Kuma mai biyayya ga uwãta, kuma bai sanya ni mai kaushin zũciya ba marashin alhẽri." (Alkur'ani 19:31-32)*

*"Kuma aminci ya tabbata a gare ni a rãnar da aka haife ni da rãnar da nake mutũwa da rãnar da ake tãyar da ni inã mai rai." (Alkur'ani 19:33)*

Karin ayoyi biyu sun fada cewa Yesu ya rigaya ya mutu, ko da shi ke ba a bayyana a cikin wasu juyin Alkur'ani na Turanci ba.

*A lõkacin da Ubangiji Ya ce: "Ya Ĩsa! Lalle NĨ Mai karɓar ranka ne, kuma Mai ɗauke ka ne zuwa gare Ni, kuma Mai tsarkake ka daga waɗanda suka kãfirta, kuma Mai sanya waɗanda suka bĩ ka a bisa waɗanda suka kãfirta har Rãnar ¡iyãma. Sa'an nan kuma zuwa gare Ni makõmarku take, sa'an nan in yi hukunci a tsakãninku, a cikin abin da kuka kasance kuna sãɓã wa jũna. (Alkur'ani 3:55)*

Waɗansu juyi na wannan aya na kai tsaye da kuma bayyana ma'ana na ayar:
*Kuma lokacin da Allah ya ce: "O, Ĩsa, Zan karasa lokacin zamanka (a duniya)…"* (Juyin M. H. Shakir).

Kalman Larabci da an mora a wannan ayar (farasar karasa) shi ne *mutawaffeeka,* wanda ma'anar na iya zama cewa zai mutu a jiki, wanda shi ne mafi manufa na ma'anar kalman, ko kuwa cewa ya ziyarci Allah a cikin barci sa'an nan ya koma ga jikinsa.

Kalma mai ma'ana irin ɗaya ne an yi amfani da shi a cikin Alkur'ani 5:117 – inda ta ce, "Ka ɗauke ni sama":
*"Ban faɗa musu ba fãce abin da Ka umurce ni da shi; watau: 'Ku bauta wa Allah Ubangijina kuma Ubangijinku;' kuma nã kasance mai shaida a kansu matuƙar nã dawwama a cikinsu, sa'an nan a lõkacin da Ka karɓi raina Kã kasance Kai ne mai tsaro a kansu, kuma Kai, a kan dukkan kõme, Halartacce ne." (Alkur'ani 5:117)*

Fassarar Turanci da waɗannan ayoyi biyu daga Larabci da alama ya canja ta wurin shekaru inda ma'anar kalman Larabcin ta mutu har ba ya bayyananne kuma a wasu sabobin fassara.

| Fassara | Alkur'ani | Nassi |
|---|---|---|
| M. Muhammadu Ali 1917 | 3:55 | *"...Zan sa ka ka mutu sa'an nan In daukaka ka a gabana...."* |
| | 5:117 | *"...Amma a lokacin da Ka sa Na mutu..."* |
| Sher Ali 1955 | 3:55 | *"...Zan sa ka ka mutu a jiki sa'an nan in daukaka ka zuwa gareni...."* |
| | 5:117 | *"...Amma tun da Ka sa na mutu ba..."* |
| M. H. Shakir 1983 | 3:55 | *"...Zan karasa zamanin zamanka (aduniya) sa'an nan In sa Ka hawa zuwa gare Ni...."* |
| | 5:117 | *"...Amma a lokacin da Ka sa Na mutu...."* |
| Muhammadu Asa 1980 | 3:55 | *"...Lalle, Zan sa ka ka mutu, kuma Zan daukaka ka zuwa gare Ni....".* |
| | 5:117 | *"...Amma tun da Ka sa Na mutu..."* |
| Rashad Khalifa 1981 | 3:55 | *"...Ina karasa rayuwarka, In ta da Kai zuwa gare Ni..."* |
| | 5:117 | *"...Lokacin da ka kasara rayuwarta a duniya...."* |
| Mohammadu da Osama El-Shinawy 1978 | 3:55 | *"...O, Yesu, hakika Zan dauke Ka In kuma tashe Ka zuwa gare Ni..."* |
| | 5:117 | *"...Amma a lokacin da Ka dauke Ni sama..."* |

Bugu da kari, Alkur'ani ya nuna cewa Yesu ya mutu kamar sauran manzanni da an aiko daga wurin Allah:

*Kuma Muhammadu bai zama ba face manzo lalle ne manzanni sun shũde a gabãninsa…. (Alkur'ani 3:144)*

**Sabon Alkawari na Littafi Mai Tsarki na Kunshe da Cikakken Labarai na Fari da na Biyu daga Shaidu da suka Kasance a Ranar Gicciye da Mutuwar Yesu.**

Za a iya karanta wadannan cikin: *Matiyu 27:1-56; Markus 15:1-41; Luke 22:47-23:19* da kuma *Yahaya 18:1-19:37.* Sun bayyana yadda aka kama Yesu, an yi masa tambayoyi, yadda masu mulki suka duke shi, aka sa masa rawanin kaya, sojojin Roma suka yi masa ba'a, sun tofa masa yau sannan aka yanke masa hukuncin kisa. Sun kuma bayyana dukan matakai lokacin da aka dauke zuwa wurin kisa, yadda aka soke shi da kusoshi a hannuwansa da kafaffunsa da yadda aka soke shi a kwibi domin a tabbatar da mutuwarsa, a dalilin ne nan da nan sai ga jini da ruwa suka gudano daga jikinsa. Bugu da kari, an rubuta sunayen wadansu da suka kasance a ranar gicciye da mutuwar Yesu.

**Linjila (Bishara) Ya Fada Abin da Yesu ya yi Magana a Bisa Gicciye, inda Ya:**

- Roki Allah ya gafarta wa wadanda suka gicciye shi domin ba su san abin da suke yi ba *(dubi Luka 23:34)*
- Yi alkawari wa daya daga cikin masu laifi da aka gicciye tare da shi cewa yau ma za ka kasance tare da ni a Firdausi *(dubi Luka 23:43)*
- Tambayi Allah don me ya yashe shi *(dubi Matiyu 27:46; Markus 15:34)*
- Gaya wa uwa tasa Maryamu cewa Yahaya, almajiransa, shi ne danta sa´nnan ya gaya wa Yahaya cewa Maryamu ita ce mahaifiyarsa *(dubi Yahaya 19:26-27)*
- Ikirari cewa yana jin kishirwa *(dubi Yahaya 19:28)*
- Nuna cewa manufarsa a duniya ya cika lokacin da ya yi shelar: *"An gama" (Yahaya 19:30)*
- Kuma sa'ad da yana mutuwa, ya ce, *"Ya Uba, na sa ruhuna a ikonka" (Luka 23:46)*

**Labarai na Linjila (Bishara) Sun Hada da Bayyani akan Abin da ya Faru a Ranar da Yesu ya Mutu a Bisa Gicciye:**

*To, tun daga tsakar rana, duhu ya rufe ƙasa duka, har zuwa ƙarfe uku na yamma... Sai Yesu ya sāke ɗaga murya da ƙarfi, sa'an nan ya sǎki ransa. Sai labulen da ke cikin Haikalin ya tsage gida biyu, daga sama har ƙasa. Ƙasa ta yi girgiza, duwatsu kuma suka tsattsage. Aka bubbuɗe kaburbura, tsarkaka da yawa da ke barci kuma suka tashi... Sa'ad da jarumin da waɗanda ke tare da shi suna tsaron Yesu suka ga rawar ƙasa da kuma abin da ya auku, sai duk tsoro ya kama su, suka ce, "Hakika wannan Ɗan Allah ne!" (Matiyu 27:45, 50-52, 54)*

**Lura! Shaidu ne suka Rubuta Linjila (Bishara) a lokacin da yawancin mutanen da suka kasance a wurin aukuwar suna raye kuma sun tuna da duk abin da ya faru.**

**Annabawan Tsohon Alkawari sun yi annabcin mutuwar Almasihu (Masiha) sun kuma bayyana yadda da kuma dalilin da zai mutu:**

Zabura ta 22 ya fara sosai daidai da kalmomin da Yesu daga murya a bisan gicciye: *Ya Allahna, ya Allahna, Don me ka yashe ni? (Zabura 22:1)*

Ko da shi ke an rubuta Zabura ta 22 wajen sheƙaru dubu kafin wancan batun ya faru, ta bayyana cikakke abin da ya faru lokacin da aka gicciye Yesu:
*Ƙarfina ya ƙare, Ya rabu da ni kamar ruwan da ya zube ƙasa. Dukan gaɓoɓina sun guggulle, Zuciyata ta narke kamar narkakken kākin zuma. Maƙogwarona ya bushe kamar ƙura, Harshena kuma na liƙe wa dasashina na sama. Ka bar ni matacce cikin ƙura. Ƙungiyar mugaye na kewaye da ni, Suka taso mini kamar garken karnuka, Suka soke hannuwansa da ƙafafuna. Ana iya ganin ƙasusuwana duka. Magabtana suka dube ni, suka zura mini ido. Suka rarraba tufafina a tsakaninsu, Suka jefa kuri'a a kan babbar rigata. (Zabura 22:14-18)*

Bisharar Yahaya ta bayyana yadda wannan annabcin ya cika, har ma da abin da ya faru da tufafin Yesu:

*Bayan soja sun gicciye Yesu, suka ɗibi tufafinsa, suka kasa kashi huɗu, kowane soja ya ɗauki kashi guda. Suka kuma ɗauki taguwa tasa, taguwar kuwa ba ɗinki, saƙa ɗaya ce gudanta. Sai suka ce wa juna, "Kada mu tsaga ta, sai dai mu yi kuri'a a kanta, mu ga wanda zai ci." Wannan kuwa domin a cika Nassi ne cewa, "Sun raba tufafina a junansu, Taguwata kuwa suka yi kuri'a a kanta" (Yahaya 19:23-24)*

Annabi Ishaya ya bayyana a sura 53 dalilin da Almasihu (Masiha) zai mutu:

*Muka raina shi, muka ƙi shi, Ya daure da wahala da raɗaɗi. Ba wanda ya ko dube shi. Muka yi banza da shi kamar shi ba kome ba ne. Amma ya daure da wahala wadda a ainihi tamu ce, Raɗaɗin da ya kamata mu ne za mu sha shi. Mu kuwa muna tsammani wahalarsa Hukunci ne Allah yake yi masa. Amma aka yi masa rauni saboda zunubanmu, Aka daddoke shi saboda muguntar da muka aikata. Hukuncin da ya sha ya 'yantar da mu, Dukan da aka yi ta yi masa, ya sa muka warke. Dukanmu muna kama da tumakin da suka ɓata, Kowannenmu ya kama hanyarsa. Sai Ubangiji ya sa hukunci ya auko a kansa, Hukuncin da ya wajaba a kanmu... Aka kama shi, aka yanke masa shari'a, Aka tafi da shi domin a kashe shi, Ba wanda ya kula da ƙaddararsa. Aka kashe shi saboda zunubin mutanenmu. (Ishaya 53:3-6, 8)*

**Yesu ya gaya wa almajiransa game da sannanen mutuwarsa da tashinsa daga matattu:**

*Tun daga lokacin nan Yesu ya fara bayyana wa almajiransa, lalle ne ya tafi Urushalima, ya sha wuya iri iri a hannun shugabanni da manyan firistoci da malaman Attaura, har a kashe shi, a rana ta uku kuma a tashe shi. (Matiyu 16:21)*

*Yesu na tafiya Urushalima, ya ɗauki almajiran nan goma sha biyu waje ɗaya. Suna tafiya ke nan sai ya ce musu, "To, ga shi, za mu Urushalima, za a kuma ba da Ɗan Mutum ga manyan firistoci da malaman Attaura, za su kuwa yi masa hukuncin kisa, su bashe shi ga al'ummai, su yi masa*

*ba'a, su yi masa bulala, su kuma gicciye shi. A rana ta uku kuma za a tashe shi." (Matiyu 20:17-19)*

Dubi kuma: *Matiyu 12:38-40; 16:1-4; 17:22-23; Markus 8:31-32; 9:31; 10:33; Luka 9:22.*

**An yi la'akari cewa mutuwar Yesu shi ne mafi kyau a rubutaccen aukuwa cikin tarihin da,** ba kawai saboda cikakken bayyana na aukuwa a cikin Linjila (Bishara) Hudu na Sabon Alkawari ba, amma kuma saboda ayyukan marubutan tarihin Romawa, Yahudawa da kuma Helenewa. Bugu da kari ga wannan, dukan birnin Urushalima suna sane da wannan aukuwan. An rubuta dukan lokacin – tun lokacin da Yesu yana tare da almajiransa a wani wuri da ake kira Getsamani a inda aka bashe shi aka kuma kama shi, har sai ya mutu a bisa gicciye aka kuma sa shi a kabari.

Da yake masu mulki suna da sanin abin Yesu ya fada wa almajiransa game da tashinsa daga matattu, aka hatimce kabarin aka kuma rufe da babban dutse and umarci sojan Romawa su yi tsaronta. Duk da wannan, a rana ta uku, aka same kabarin a bude ba komai kuma sannan babu wurin da aka sami jikin Yesu. Wannan faruwan an rubuta shi a Bisharar Matiyu:

*Sai kuwa aka yi wata babbar rawar ƙasa, domin wani mala'ikan Ubangiji ne ya sauko daga Sama, ya zo ya mirgine dutsen, ya zauna a kai. Kamanninsa na haske kamar walƙiya, tufafinsa kuma farare fat kamar dusar ƙanƙara. Saboda tsoronsa sai masu tsaro suka ɗau makyarkyata, har suka yi kamar sun mutu. (Matiyu 28:2-4)*

Masu Mulki suka kirkira labari domin su bayyana dalilin da ya sa jikin Yesu ya bata:

*... sai waɗansu daga cikin sojan nan suka shiga birni, suka ba manyan firistoci labarin da ya auku. Su kuwa da suka taru da shugabannin jama'a suka yi shawara, sai suka ba sojan kuɗi masu tsoka, suka ce, "Ku faɗa wa mutane almajiransa ne suka zo da daddare suka sace shi kuna barci. In kuwa labarin nan ya kai ga kunnen mai mulki, mā rarrashe shi,*

*mu tsare ku daga wahala." Sai suka karɓi kuɗin, suka yi yadda aka koya musu. Wannan magana kuwa, ta bazu cikin Yahudawa har ya zuwa yau. (Matiyu 28:11-15)*

**Mala'iku sun yi shelar tashin Yesu daga matattu:**
*A ranar farko ta mako kuwa, da asussuba, suka je wurin kabarin da kayan ƙanshi da suka shirya. Sai suka tarar an mirgine dutsen daga kabarin. Suka shiga ciki, amma ba su sami jikin Ubangiji ba. Tun suna cikin damuwa da abin, sai kawai ga waɗansu mutum biyu a tsaye a kusa da su, saye da tufafi masu ƙyalƙyali. Don tsoro, matan suka sunkuyar da kansu a ƙasa. Mutanen suka ce musu, "Don me kuke neman rayayye a cikin matattu? Ai, ba ya nan, ya tashi. Ku tuna yadda ya gaya muku tun yana Galili cewa, 'Lalle ne a ba da Ɗan Mutum ga mutane masu zunubi, a gicciye shi, a rana ta uku kuma ya tashi.' " (Luka 24:1-7)*

Jim kaɗan bayan haka, Yesu ya bayyana ga mabiyansa, da farko ga matan da sun zo wurin kabarin sa'annan ga almajiransa daga baya:
*A ran nan da magariba, ranar farko ta mako, ƙofofin ɗakin da almajiran suke ciki na kulle don tsoron Yahudawa, sai ga Yesu ya zo ya tsaya a tsaka, ya ce musu, "Salama alaikun!" Da ya faɗi haka, ya nuna musu hannuwansa da kwiɓinsa. Sai almajiran suka yi farin ciki da ganin Ubangiji. (Yahaya 20:19-20)*

Ɗaya a cikin almajiran, Toma, wanda ba ya nan a lokacin, ya furta rashin bangaskiya:
*"In ban ga gurbin ƙusoshi a hannuwansa ba, in sa yatsata a gurbin ƙusoshin, in kuma sa hannuna a kwiɓinsa ba, ba zan ba da gaskiya ba." (Yahaya 20:25)*

Bayan mako ɗaya, sa'ad da Yesu ya bayyana ga almajiransa, ya juyo ga Toma ya ce:
*"Sa yatsarka nan, ka ji hannuwansa. Miƙo hannunka kuma ka sa a kwiɓina. Kada ka zama marar ba da gaskiya, sai dai mai ba da gaskiya." (Yahaya 20:27)*

Bayan tashin Yesu daga matattu, Bitrus ya ba da waɗannan jawabi a Urushalima:
*"Ya ku 'yan'uwa, Isra'ilawa, ku ji wannan magana. Yesu Banazare, mutumin da Allah ya tabbatar muku cewa shi yardajjensa ne, ta mu'ujizai, da abubuwan al'ajabi, da alamu waɗanda ya yi ta wurinsa a cikinku, kamar yadda ku kanku kuka sani, shi Yesun nan fa, an ba da shi bisa ƙaddarar Allah da rigyasaninsa, ku kuwa kuka gicciye shi, kuka kashe shi, ta hannun masu zunubi... Yesun nan kam, Allah ya tashe shi daga matattu, mu kuwa duk Shaidu ne ga haka. (Ayyukan Manzanni 2:22-23, 32)*

Babu ko shakka a tunanin almajirai cewa Yesu ya mutu a yanzu kuma sun ga tashinsa daga matattu. Bitrus ya rubuta a wani wasikarsa:
*Domin Almasihu ma ya mutu sau ɗaya tak ba ƙari, domin kawar da zunubanmu, mai adalci saboda marasa adalci, domin ya kai mu ga Allah. An kashe shi a jiki, amma an rayar da shi a ruhu. (1 Bitrus 3:18)*

*"Shi kansa ya ɗauke zunubanmu a jikinsa a kan gungume, domin mu yi zamanmu matattu ga zunubi, rayayyu kuma ga adalci…" (1 Bitrus 2:24)*

A lokacin kwanakin arba'in Yesu ya bayyana ga almajiransa da kuma waɗansu a lokaci daban-daban:
*Sa'an nan ya bayyana ga 'yan'uwa fiye da ɗari biyar a lokaci guda, yawancinsu kuwa suna nan har yanzu, amma waɗansu sun yi barci. (1 Korantiyawa 15:6)*

Kuma yawanci suna nan a lokacin da ya hau cikin Sama a gaban idonsu:
*Da ya faɗi haka, suna cikin dubawa, sai aka ɗauke shi Sama, wani gajimare ya tafi da shi, ba su ƙara ganinsa ba. Suna cikin zuba ido a sama, shi kuma yana tafiya, sai ga mutum biyu tsaye kusa da su, saye da fararen tufafi. Sai suka ce, "Ya ku mutanen Galili, don me kuke tsaye kuna duban sama? Yesun nan da aka ɗauke daga gare ku aka kai shi zuwa Sama, zai komo ne ta yadda kuka ga tafiyarsa zuwa Sama." (Ayyukan Manzanni 1:9-11)*

A yanzu da almajiran sun ga tashin Yesu daga matattu, ba su sake jin tsoro ba a maimaikon haka, sun karfafu da wannan sabuwar aukuwa. Da a ce suna da ɗan shakkan tashin Yesu daga matattu, daidai ne a yi zaton cewa ba za su sadaukar da rayukansu ga yadda Bishara ba, da haka su kasaɗar da ransu ga kisa ba. Haka kuma, ba za su kaga irin wannan labari ba a inda mata ne suka zama shaidun farko na tashinsa daga matattu, saboda hujja na cewa ba a yin la'akari da ingancin shaida na mata a wancan lokaci.

**Bugu da kari ga Sabon Alkawari na Littafi Mai Tsarki, waɗansu takardun tarihi suka kasance a kan mutuwar Yesu, har da:**
*Littafin Tarihi (Littafi na 15, Sura 44),* wanda Tacitus, mai ilmin tarihin Romawa, Sanata kuma, ya rubuta a shekara ta 116 AD, inda ya yi maganar gicciyen Yesu bisa ga umurnin Buntus Bilatus.
*Tsofofin gine-ginen Yahudawa (Littafi na 18, Sura 3:3)* da Josephus, mai ilmin tarihin Yahudawa a karni na fari ya rubuta, ya kuma ambata Yesu da yadda Bilatus ya gicciye shi a cikin takardun rubutun tarihinsa.

Waɗansu masu ilmin tarihi kamar su Bahelene Thallus da Phlegon nan Tralles sun rubuta game da babban duhu da tsawon-awa-uku da ya kasance a ranar da an gicciye Yesu, wanda shi ne cikawar annabcin Amos a cikin Tsohon Alkawari:

*"A wannan lokaci rana za ta fāɗi da tsakar rana, Duniya ta duhunta da rana kata... Za ku yi makoki kamar iyayen da suka rasa tilon ɗansu. Ranan nan mai ɗaci ce har ƙarshe." (Amos 8:9-10)*

***Likkafanin Turin*** *6), 7)* ya goyi bayan labari wanda ɗukan Linjila (Bishara) hudu sun bayyana, game da abin da ya faru bayan an saukar da Yesu daga gicciye. Yusufu, mutumin Arimatiya, mamba na Majalisa, ya roki Bilatus ya ba shi jikin Yesu, ya ɗauki jikin, ya sa shi a sabuwar likkafanin linin ya kuma sa shi a wani sabon kabari *(dubi Matiyu 27:57-60; Markus 15:42-46; Luka 23:50-53; Yahaya 19:38-42).* Linjila (Bishara) ya ba da rahoto cewa ko da yake jikin Yesu ya tafi daga kabarin, an bar likkafanin a baya *(dubi Luka 24:12; Yahaya 20:1-8).* An yi imani cewa Likkafanin Turin kwarai shi ne wannan likkafanin linin da aka nannade jikin Yesu da shi. Masanan kimiyya da yawa sun bincika wannan likkafanin sosai. Lokacin da an ɗauka hoton, sai akasi na baki da fari su nuna a fili siffar jiki tsirara wanda aka gicciye. Su akasin sun nuna tabon jini inda aka buga kusoshi a hannaye da kafafu na jikin, a gefen jikin inda aka soka da kuma ta kansa inda aka sa rawanin kaya. An kuma iya ganin fuskar a fili saboda walkiya da yake samu daga jikin da aka sa a wannan likkafanin linin. Bugu da kari, akasin sun nuna cewa babu ko wani kasusuwan jikin da an karya ba.

Bisa ga al'ada, akan karye kafafun waɗanda aka azabtar lokacin da an yanke shawarar gaggauta mutuwarsu kamar yadda aka yi nufi a yanayin Yesu:

*Amma da suka zo wurin Yesu, suka kuma ga ya riga ya mutu, ba su karya ƙafafunsa ba. Sai dai ɗaya daga cikin sojan nan ya soke shi da mashi a kwiɓi, nan da nan sai ga jini da ruwa suka gudano. Wanda ya gani ɗin kuwa shi ya ba da shaida kan haka, shaida tasa kuwa gaskiya ce, ya kuma san gaskiya yake faɗa, domin ku ma ku ba da gaskiya. Wannan kuwa don a cika Nassi ne cewa, "Kashinsa ɗaya ba za a karya ba." Wani Nassi kuma ya ce, "Za su dubi wanda suka soka." (Yahaya 19:33-37)*

Yawancin masana a yau suna iƙirari cewa tarihi ta nuna gaskiya Yesu ya mutu a bisa gicciye kuma waɗanda suka bincika tashinsa daga matattu sun yi jayayya cewa an iya furta ba tare da shakkar sanin ya kamata ba cewa ya tashi daga matattu, a kan gagarumin tasiri da tashinsa yake da shi a rayuwar mabiyansa.

**Don haka, amsoshi ga tambaya ko Yesu ya mutu a bisa gicciye suna kamar haka:**

| **Littafi Mai Tsarki Tsohon Alkawari**<br>**I** | **Littafi Mai Tsarki Sabon Alkawari**<br>**I** | **Wađansu Tushe na Da**<br>**I** | **Alkur'ani A'a**<br>**I, cewa ya mutu** |
|---|---|---|---|
| Annabawa da yawa sun yi annabcin mutuwar Almasihu:<br>*Ishaya (Sura 53)*<br>*Dawuda (Zabura 22)*<br>*Amos (8:9-10)*<br>*Zakariya (12:10)* | Mashaidi da yawa sun bi Yesu har zuwa ƙarshe, sun tsaya a wurin gicciye, sun duba da kuma sauraronsa a sa'o'insa na ƙarshe:<br>*Matiyu 27:1-66*<br>*Markus 15:1-41*<br>*Luka 22:47-23:56*<br>*Yahaya 18:1-19:42* | Shaida da aka samu a rubuce-rubucen masu ilmin tarihi na karni ta fari da ta biyu:<br>*Tacitus, Josephus, Lucian, Talmud na Babila.* | A'a:<br>Yesu ba mutu a bisa gicciye ba:<br>*Alkur'ani 4:157-158*<br><br>I:<br><u>Ya nuna Yesu zai mutu:</u><br>*Alkur'ani 19:30-31,33*<br><u>Ya tabbatar ya mutu:</u><br>*Alkur'ani 3:55*<br>*Alkur'ani 5:117*<br>*Alkur'ani 3:144* |

*Babi Na 3*

# Yesu Shi ne Ɗan Allah?

Alkur’ani da Littafi Mai Tsarki gaba ɗaya suna da bambancin ra’ayi a kan tambaya ko Yesu ne Ɗan Allah ko babu.

**Alkur’ani ya dai bayyana cewa Yesu annabi ne da kuma Almasihu (Masiha) kuma ya kasance ta wurin allahntaka. Duk da haka, bai amince ko yarda cewa zai iya zama Ɗan Allah ba:**

*Kuma ka ambaci Maryamu a cikin Littãfi, a lõkacin da ta tsallake daga mutãnenta a wani wuri, a gẽfen gabas. Sa'an nan ta riƙi wani shãmaki daga barinsu. Sai Muka aika rũhinMu zuwa gare ta. Sai ya bayyana a gare ta da siffar mutum madaidaci. Ta ce: "Lalle nĩ inã nẽman tsari ga Mai, rahama daga gare ka, idan ka kasance mai tsaron addini!" Ya ce: "Abin sani kawai, ni Manzon Ubangijinki ne dõmin in bãyar da wani yãro tsarkakke gare ki." Ta ce: "A inã yãro zai kasance a gare ni alhãli kuwa wani mutum bai shãfe ni ba, kuma ban kasance kãruwa ba?" Ya ce: "Kamar wancan Ubangijinki Ya ce. Shĩ, a gare Ni mai sauƙi ne. Kuma dõmin Mu sanya shi wata alãma ga mutãne, kuma wata rahama ce daga gare Mu.' Kuma abin yã kasance wani al'amari hukuntacce." (Alkur’ani 19:16-21)*

*Lalle ne misãlin Ĩsã a wurin Allah kamar misãlin Ãdama ne, (Allah) Yã halitta shi daga turɓãya, sa'an nan kuma Ya ce masa: "Ka kasance: "Sai yana kasancewa. (Alkur’ani 3:59)*

*Bã ya kasancẽwa ga Allah Ya riƙi wani ɗã. Tsarki ya tabbata a gare shi! Idan Yã hukunta wani al'amari sai kawai Ya ce masa, "Kasance." Sai ya dinga kasan cẽwa. (Alkur'ani 19:35)*

*Kuma suka ce: "Mai rahama Yã riƙi ã!" Lalle ne haƙĩka kun zo da wani abu mai girman mũni. Sammai sunã kusa su tsattsage sabõda shi, kuma ƙasa ke kẽce kuma duwãtsu su faɗi sunã karyayyu. Dõmin sun yi da'awar ɗã ga Mai rahama. Alhãli bã ya kamata ga Mai rahama ya riƙi wani ɗã. (Alkur'ani 19:88-92)*

*Mafarin halittar sammai da ƙasa. Yãya ɗã zai zama a gare Shi alhãli kuwa mãta ba ta kasance ba, a gare Shi, kuma Ya halitta dukkan, kõme, kuma Shĩ, game da dukan kõme, Masani ne? (Alkur'ani 6:101)*

*"Kuma Nasãra suka ce: "Masĩhu ɗan Allah ne." Wancan zancensu ne da bãkunansu. Sunã kamã da maganar waɗanda suka kãfirta daga gabãni. Allah Yã la'ance su! Yãya aka karkatar da su? (Alkur'ani 9:30)*

*Suka ce: "Allah Ya riƙi ɗa." Tsarkinsa yã tabbata! Shi ne wadãtacce Yanã da mallakar abin da yake, a cikin sammai da abin da yake a cikin ƙasa, A wurinku bãbu wani dalĩli game da wannan! Shin, kunã faɗar abin da ba ku sani ba game da Allah? (Alkur'ani 10:68)*

*Kuma Ya yi gargaɗi ga waɗanda suka ce: "Allah yanã da ɗa." Ba su da wani ilmi game da wannan magana, kuma iyãyensu bã su da shi, abin da ke fita daga bãkunansu ya girma ga ya zama kalmar faɗa! Ba su faɗan kõme fãce ƙarya. (Alkur'ani 18:4-5)*

**Littafi Mai Tsarki a ɗaya hannun ya yi ikirari nassosi da yawa cewa Yesu ne Ɗan Allah.**

**I cikin annabce-annabcen Tsohon Alkawari:**
*"Zan yi shelar abin da Ubangiji ya ce mini, 'Kai ɗana ne, Yau ne na zama mahaifinka." (Zabura 2:7)*

*Ku yi mubaya'a da Ɗan ...Albarka ta tabbata ga dukan masu zuwa gare shi neman mafaka!" (Zabura 2:12)*

*"Zan cika zuriyar Dawuda da mutanen Urushalima da ruhun tausayi da na addu'a. Za su dubi wanda suka soke shi, har ya mutu. Za su yi makoki dominsa kamar waɗanda aka yi musu rasuwar ɗan farinsu." (Zakariya 12:10)*

**A cikin Sabon Alkawari:**
*A wata na shida Allah ya aiko mala'ika Jibra'ilu zuwa wani gari a ƙasar Galili, wai shi Nazarat, gun wata Budurwa da aka ba da ita ga wani mutum mai suna Yusufu, na zuriyar Dawuda, sunan budurwar kuwa Maryamu. Sai mala'ikan ya je wurinta, ya ce, "Salama alaikun, yake zaɓaɓɓiya, Ubangiji yana tare da ke!" Amma ta damu ƙwarai da maganar, ta yi ta tunani ko wannan wace irin gaisuwa ce. Mala'ikan kuma ya ce mata, "Kada ki ji tsoro. Maryamu, kin sami tagomashi a wurin Allah. Ga shi kuma, za ki yi ciki, ki haife ɗa, ki kuma sa masa suna Yesu. Zai zama mai girma, za a kuma kira shi Ɗan Maɗaukaki. Ubangiji Allah zai ba shi kurshiyin ubansa Dawuda, Zai kuma mallaki zuriyar Yakubu har abada, Mulkinsa kuwa ba shi da matuƙa." Sai Maryamu ta ce wa mala'ikan, "Ƙaƙa wannan zai yiwu, tun da yake ba a kai ni ɗaki ba?" Mala'ikan ya amsa mata ya ce, "Ruhu Mai Tsarki zai sauko miki, Ikon Maɗaukaki kuma zai lulluɓe ki. Saboda haka Mai Tsarkin nan da za a Haifa, za a kira shi Ɗan Allah." (Luka 1:26-35)*

*Farkon bisharar Yesu Almasihu, Ɗan Allah, ke nan. (Markus 1:1)*

*...wadda Allah ya yi alkawari tun dā, ta bakin annabawansa a cikin Littattafai masu tsarki. Bishara ɗin nan a kan Ɗansa ce, Ubangijinmu Yesu Almasihu, wanda ga jiki shi zuriyar Dawuda ne, amma ga tsarkinsa na ruhu shi Ɗan Allah ne, da iko aka ayyana shi haka ta wurin tashinsa daga matattu: Yesu Almasihu Ubangijinmu. (Romawa 1:2-4)*

*To, shi wannan da muka ji, muka kuma gani, shi ne dai muke sanar da ku, domin ku ma ku yi tarayya da mu. Hakika kuwa tarayyar nan tamu da Uba ne, da kuma Ɗansa Yesu Almasihu. (1 Yahaya 1:3)*

*In kuwa muna zaune a haske, kamar yadda shi yake cikin haske, muna tarayya da juna ke nan, jinin Yesu Ɗansa kuma yana tsarkake mu daga dukkan zunubi. (1 Yahaya 1:7)*

*To, tun da yake muna da Babban Firist mai girma, wanda ya ratsa sammai, wato Yesu Ɗan Allah, sai mu tsaya a kan abin da muka bayyana yarda gare shi. (Ibraniyawa 4:14)*

*A zamanin dā, Allah ya yi wa kakannin kakanninmu magana ta hanyoyi masu yawa iri iri, ta bakin annabawa, amma a zamanin nan na ƙarshe, sai ya yi mana magana ta wurin Ɗansa, wanda ya sa magājin kome, wanda ta wurinsa ne kuma ya halicci duniya. Shi ne hasken ɗaukakar Allah, ainihin kamannin zatinsa kuma, shi kuma yana a riƙe da dukan abubuwa ta ikon faɗarsa. Bayan da ya tsarkake zunubanmu, sai ya zauna a dama da Maɗaukaki a can Sama. Ta haka yake da fifiko a kan mala'iku, kamar yadda sunansa da ya gāda yake da fifiko nesa a kan nasu. Domin kuwa wane ne a cikin mala'iku Allah ya taɓa ce wa, “Kai Ɗana ne...?” (Ibraniyawa 1:1-5)*

Yesu ya Fada:

*“Ubana yana aiki har yanzu, ni ma ina yi”. Don haka, Yahudawa suka ƙara nema su kashe shi, ba don ya keta Asabar kaɗai ba, har ma domin ya ce Allah Ubansa ne, wato, yana daidaita kansa da Allah. (Yahaya 5:17-18)*

*“In kuwa Ɗan ya ‘yanta ku, za ku ‘yantu, ‘yantuwar gaske.” (Yahaya 8:36)*

*“Ni da Uba ɗaya muke.” (Yahaya 10:30)*

Misalai na Yesu a cikin *Matiyu 21:33-39* da *Matiyu 22:1-10* duka game da kansa a matsayin Ɗan da kuma game da Ubansa a matsayin Maigidan da kuma Sarkin. A cikin dukan waɗannan misalai, an aiki bayin ga manufa, da dai dai, amma dukansu an yi musu duka, wulakanci ko kuwa kisa.

*"...Daga baya sai ya aiki ɗansa gare su, yana cewa, "Sā ga girman ɗana." (Matiyu 21:37)* Duk da haka, a ƙarshen wancan misali aka kashe ɗan kuma.

**Muguyen ruhohi sun san cewa Yesu Ɗan Allah ne:**

*Baƙaƙen aljannu kuwa, duk sa'ad da suka gan shi, sai su fāɗi gabansa suna kururuwa, suna cewa, "Kai Ɗan Allah ne." Sai ya kwaɓe su ƙwarai kada su bayyana shi. (Markus 3:11-12)*

*Markus 5:1-20* ya ba da labarin wani mutum, wanda mugun ruhu ya yi masa azaba, wanda kuma Yesu ya 'yantar:

*Da dai ya hango Yesu, sai ya sheƙo a guje ya fāɗi a gabansa, ya ƙwala ihu ya ce, "Ina ruwanka da ni, Yesu Ɗan Allah Maɗaukaki? Na gama ka da Allah, kada ka yi mini azaba." Ya faɗi haka ne domin Yesu ya ce masa, "Rabu da mutumin nan, kai wannan baƙin aljan!" (Markus 5:6-8)*

A fili yake cewa Yesu ya yi la'akari da kansa shi Ɗan Allah ne ta wurin yadda ya yi magana a lokacin da almajiransa sun so su hana kama shi:

*Kuna tsammani ba ni da ikon neman taimake gun Ubana ba, nan da nan kuwa ya aiko mini fiye da rundunar mala'iku goma sha biyu? To, ta yaya ke nan za a cika Littattafai a kan lalle wannan abu ya kasance?" (Matiyu 26:53-54)*

**Bisa ga Nassi, Almasihu da Ɗan Allah ɗaya ne, mutum ɗaya kuma:**

*"Amma ku fa, wa kuke cewa, nake?" Sai Bitrus ya amsa, ya ce, "Kai ne Almasihu, Ɗan Allah Rayayye." Yesu ya amsa masa ya ce, "Kai mai Albarka ne, Saminu, ɗan Yunusa! Domin ba ɗan adam ne ya bayyana maka wannan ba, sai dai Ubana da yake cikin Sama." (Matiyu 16:15-17)*

*Amma Yesu na shiru. Sai babban firist ya ce masa, "Na gama ka da Allah Rayayye, ka faɗa mana ko kai ne Almasihu, Ɗan Allah." (Matiyu 26:63)*

*Amma an rubuta waɗannan ne, domin ku ba da gaskiya Yesu shi ne Almasihu, Ɗan Allah, ta wurin gaskatawa kuma ku sami rai a cikin sunansa. (Yahaya 20:31)*

An Yi wa Yesu Ba'a a Bisan Gicciye:
*"Ya ceci waɗansu, ya kuwa kasa ceton kansa. Ai, Sarkin Isra'ila ne, yǎ sauko mana daga gicciyen yanzu, mu kuwa mā gaskata da shi. Yā dogara ga Allah, to, Allah ya cece shi mana yanzu, in dai yana sonsa, don ya ce shi Ɗan Allah ne." (Matiyu 27:42-43)*

A Littafin ƙarshe na Littafi Mai Tsarki, Littafin Wahayin Yahaya, Yesu ya gabatar da kansa wa Yahaya, almajirinsa, a matsayin Ɗan Allah:
*"Ga maganar Ɗan Allah…" (Wahayin Yahaya 2:18)*

**Domin La'akari:**
Tun da duka Alkur'ani da Littafi Mai Tsarki suka bayyana haifuwar Yesu a matsayin abu ne na allahntaka kuma dukansu suka mika shi a matsayin Almasihu (Kristi), to ta yaya zai zama manzo na Allah kawai kamar yadda Alkur'ani ta furta? Wannan ya ja hankali ga muhimmin tambaya, me ake nufi da cewa Shi ne Almasihu?

*Babi Na 4*

# Yesu da Kansa Allah Ne?

**Littafi Mai Tsarki da Alkur'ani sun yarda cewa Allah ɗaya ne wanda ya wajaba a yi masa sujada.**

## Alkur'ani:

*Lalle ne wannan, hakĩka, shi ne lãbãri tabbatacce, kuma bãbu wani abin bautawa fãce Allah, kuma lalle ne, Allah, hakĩka, Shi ne Mabuwãyi Mai hikima. (Alkur'ani 3:62)*

*"Lalle, Nĩ Ni ne Allah. Bãbu abin bautawa fãce Ni. Sai ka bauta Mini, kuma ka tsayar da salla dõmin tuna Ni." (Alkur'ani 20:14)*

## Littafi Mai Tsarki:

Na farko a cikin dokoki goma da Musa ya karba a wurin Allah shi ne: *"Ni ne Ubangiji Allahnka wanda ya fisshe ka daga kasar Masar, daga gidan bauta. Kada ka kasance da wadansu alloli…" (Fitowa 20:2-3)*

Annabi Ishaya ya rubuta:
*…Ashe, ba ni ba ne, Ubangiji, Allah wanda ya ceci mutanensa? Ba wani Allah sai ni. (Ishaya 45:21)*

Yesu ya fada daga Nassi:

*Domin a rubuce yake cewa, “Kă yi wa Ubangiji Allahnka sujada, Shi kaɗai za ka bauta wa.” (Matiyu 4:10)*

Kuma, lokacin da an tambayi Yesu wane umarni ne mafi girma duka, ya amsa:
*“…Ku saurara, ya Isra’ila, Ubangiji Allahnmu, Ubangiji ɗaya ne. Sai ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da dukkan zuciyarka….” (Markus 12:29-30)*

**A wani hannu kuma, Littafi Mai Tsarki da Alkur’ani ba su yarda ko Yesu da kansa shi ne Allah ba, kamar sasshe na Allah a Triniti (Ukunta) – Allah Uba, Allah Da da kuma Allah Ruhu Mai Tsarki.**

## Alkur’ani:

*Yã Mutãnen Littãfi! Kada ku zurfafã a cikin addininku. Kuma kada ku faɗa, ga Allah, fãce gaskiya. Abin da aka sani kawai, Masĩ hu ĩsa ɗan Maryama Manzon Allah ne, kuma kalmarSa, yã jẽfa ta zuwa ga Maryama, kuma rũhi ne daga gare Shi. Sabõda haka, ku yi ĩmãni da Allah da manzanninSa, kuma kada ku ce, "Uku". Ku hanu (daga faɗin haka) yã fi zama alhẽri a gare ku. Abin da aka sani kawai, Allah Ubangiji ne Guda. TsarkinSa yã tabbata daga wani abin haifuwa ya kasance a gare Shi! Shĩ ne da abin da ke cikin sammai da abin da ke cikin ƙasa kuma Allah Yã isa Ya zama wakĩli. (Alkur’ani 4:171)*

*Lalle ne hakĩka waɗanda suka ce: "Lalle ne Allah, shĩne Masĩhu, ɗan Maryama," sun kãfirta. Alhãli kuwa Masĩhu yã ce: "Yã Banĩ Isrã'ĩla! Ku bauta wa Allah Ubangijina, kuma Ubangijinku." Lalle ne shĩ, wanda ya yi shirki da Allah, to, lalle ne, Allah Yã haramta masa Aljanna. Kuma bãbu wasu mataimaka ga azzãlumai. (Alkur’ani 5:72)*

*Lalle ne, hakĩka, waɗanda suka ce: "Allah na ukun uku ne," sun kãfirta, kuma babu wani abin bautãwa fãce Ubangji Guda... (Alkur’ani 5:73)*

*Kuma a lõkacin da Allah Ya ce: "Yã Ĩsã ɗan Maryama! Shin, kai ne ka ce wa mutãne, 'Ku riƙe ni, ni da uwata, abubuwan bautãwa biyu, baicin Allah?" (Ĩsã) Ya ce: "Tsarkinka yã tabbata! Bã ya kasancewa a gare ni,*

*in faɗi abin da bãbu wani hakki a gare ni. Idan nã kasance nã faɗe shi, to lalle Ka san shi, Kanã sanin abin da ke a cikin raina, kuma bã ni sanin abin da ke a cikin nufinKa. Lalle ne Kai Masanin abubuwan fake ne." (Alkur'ani 5:116)*

*Allah bai riƙi wani abin haihuwa ba, kuma bãbu wani abin bautãwa tãre da Shi. Idan haka ne (akwai abin bautawa tare da Shi), lalle ne dã kõwane abin bautawar ya tafi da abin da ya halitta, kuma lalle ne, dã waɗansu sun rinjãya a kan waɗansu, tsarki ya tabbata ga Allah, daga abin da suke siffantãwa. (Alkur'ani 23:91)*

*Kuma ka ce: "Gõdiyã ta tabbata ga Allah wanda bai riƙi ɗã ba kuma abõkin tãrayya bai kasance a gare Shi ba a cikin mulkinSa, kuma wani masõyi sabõda wulãkancin bai kasance a gare Shi ba." Kuma ka girmama Shi, girmamãwa. (Alkur'ani 17:111)*

## Littafi Mai Tsarki:

Ko da shi ke Littafi Mai Tsarki yana koyar cewa Allah ɗaya ne, ya bayyana Allah a fili a matsayin mutum uku: Allah Uba, Allah Ɗa (Yesu) da Allah Ruhu Mai Tsarki. Bari mu dubi waɗansu ayoyyi a cikin Littafi.

A labari na halittar duniya a sura ta fari na Littafi Mai Tsarki, Allah ya gabatar da kansa na farko-mutum-jam'i:
*Allah kuma ya ce, "Bari mu yi mutum cikin siffarmu, da kamanninmu…" (Farawa 1:26)*

Annabi Ishaya ya yi annabcin zuwan Almasihu (Masiha):
*Yanzu fa, Ubangiji kansa zai ba ku alama. Wata Budurwa wadda take da ciki, za ta haifi da, za a raɗa masa suna Immanuwel. (ma'anar Immanuwel shi ne Allah tare da mu) (Ishaya 7:14)*

*Jama'ar da suka yi tafiya cikin duhu, Sun ga babban haske! Suka zauna a inuwar mutuwa, Amma yanzu haske ya haskaka su… Ga shi, an Haifa mana ɗa! Mun sami yaro! Shi zai zama Mai Mulkinmu. Za a kira shi, "Mashawarci Mai Al'ajibi," "Allah Maɗaukaki," "Uba Madawwami,"*

*"Sarkin Salama. "Sarautar ikonsa za ta yi ta ci gaba, Mulkinsa zai kasance da salama kullayaumin… (Ishaya 9:2, 6-7)*

*"Ka ƙarfafa, kada kuwa ka ji tsoro! Allah yana zuwa domin ya kuɓutar da kai, Yana zuwa domin ya ɗauki fansa a kan abokan gābanka." (Ishaya 35:4-5)*

Annabi Daniyel ya sami wahayin Sama ya kuma bayyana abin da ya gani:
*"A cikin wahayi na dare, na ga wani kamar Ɗan Mutum. Yana zuwa cikin gizagizai, Ya zo wurin wanda yake Tun Fil Azal, Aka kai shi gabansa. Aka kuwa danƙa masa mulki, da ɗaukaka, da sarauta, Domin dukan jama'a, da al'ummai, da harsuna su bauta masa. Mulkinsa, madawwamin mulki ne, Wanda ba zai ƙare ba. Sarautarsa ba ta tuɓuwa." (Daniyel 7:13-14)*

**Waɗansu ayoyyi da yawa a cikin Littafi Mai Tsarki sun nuna Allahntakar Yesu:**
*Tun fil'azal akwai Kalma, Kalman nan kuwa tare da Allah yake, Kalman nan kuwa Allah ne. Shi ne dun fil'azal yake tare da Allah... Kalman nan kuwa ya zama mutum, ya zauna a cikinmu, yana mai matuƙar alheri da gaskiya. Mun kuma dubi ɗaukakarsa, ɗaukaka ce ta makaɗaicin Ɗa daga wurin Ubansa. (Yahaya 1:1-2, 14)*

Duk mutum uku na Allah a trinity sun kasance a baftismar Yesu:
*Da aka yi wa Yesu baftisma, nan da nan da ya fito daga ruwan, sai ga sama ta dāre, ya ga Ruhun Allah na saukowa da kamar kurciya, har ya sauka a kansa. Sai aka ji wata murya daga Sama ta ce, "Wannan shi ne Ɗana ƙaunataccena, wanda nake farin ciki da shi ƙwarai." (Matiyu 3:16-17)*
An rubuta wannan ma a cikin *Markus 1:9-11* da *Luka 3:21-23*

Yahaya Mai Baftisma ya ba da Shaidarsa game da Yesu:
*"Na ga Ruhu na saukowa kamar kurciya daga sama, ya kuma zauna a kansa. Dā kam, ban san shi ba, shi dai wanda ya aiko ni in yi baftisma*

*da ruwa, shi ne ya ce mini, 'Wanda ka ga Ruhun na sauko masa, yana kuma kasance a kansa, shi ne mai yin baftisma da Ruhu Mai Tsarki.' Na kuwa gani, na kuma yi shaida, cewa, wannan Ɗan Allah ne." (Yahaya 1:32-34)*

An ji irin wannan sako lokacin da Yesu ya tafi da almajiransa Bitrus, Yakubu da Yahaya, a kan dutse domin ya yi addu'a:
*Yana yin addu'a, sai kama tasa ta sāke, tufafinsa kuma suka yi fari fat, har suna ɗaukar ido. Sai ga mutum biyu suna magana da shi, wato Musa da Iliya. Sun bayyana da ɗaukaka, suna zancen ƙaura tasa ne, wadda yake gabannin yi a Urushalima... Yana faɗar haka sai wani gajimare ya zo ya rufe su. Da kuma gajimaren ya lulluɓe su suka tsorata. Sai aka ji wata murya daga cikin gajimaren, tana cewa, "Wannan shi ne Ɗana zababbena. Ku saurare shi!" (Luka 9:29-31, 34-35)*

A wasikarsa ta biyu, Bitrus ya nuna wannan aukuwa:
*Ai, ba tatsuniyoyi da aka ƙaga da wayo muka bi ba, sa'ad da muka sanar da ku ikon Ubangijinmu Yesu Almasihu, da kuma bayyanarsa, ɗaukakarsa ce muka gani muraran. Domin sa'ad da Allah Uba ya girmama shi, ya kuma ɗaukaka shi, sai murya ta zo masa daga mafificiyar ɗaukaka cewa, "Wannan shi ne Ɗana ƙaunataccena, wanda nake farin ciki da shi ƙwarai," mu ne muka ji muryar nan da aka saukar daga sama, don muna tare da shi a kan tsattsarkan Dutsen nan. (2 Bitrus 1:16-18)*

Yesu ya furta cewa shi ne Almasihu (Masiha), ta haka Ɗan Allah ne:
*Sai babban firist ɗin ya sāke tambayarsa, "To, ashe, kai ɗin nan ne Almasihu Ɗan Maɗaukaki?" Yesu ya ce, "Ni ne. Za ku kuwa ga Ɗan Mutum zauna dama ga Mai Iko, yana kuma zuwa cikin gajimare." (Markus 14:61-62)*
Wannan ya yi daidai da abin Sarki Dawuda ya rubuta a *Zabura 110:1*.

Aka Zargi Yesu da Laifin Sabo:
*Sai Yahudawa suka sāke debo duwatsu su jajjefe shi. Yesu ya amsa musu ya ce, "Na nuna muku ayyuka nagari masu yawa daga wurin Uba, a kan wanne a cikinsu za ku jajjefe ne?" Yahudawa suka amsa suka ce, "Ba*

*don wani aiki nagari za mu jajjefe ka ba, sai don sābo, don kai, ga ka mutum, amma kana mai da kanka Allah." (Yahaya 10:31-34)*

*Yahudawa suka amsa masa suka ce, "Ai, muna da Shari'a, bisa ga Shari'an nan kuwa ya wajaba a kashe shi, saboda ya mai da kansa Ɗan Allah." (Yahaya 19:7)*

Almajiri Toma ya ce wa Yesu lokacin da ya ganshi bayan tashinsa daga matattu:
*"Ya Ubangijina Allahna kuma!" Sai Yesu ya ce masa, "Wato, saboda ka gan ni ka ba da gaskiya? Albarka tā tabbata ga waɗanda ba su gani ba, amma kuwa suka ba da gaskiya." (Yahaya 20:28-29)*

Manzo Bulus ya rubuta:
*Ku ɗauki halin Almasihu Yesu, wanda, ko da yake a cikin surar Allah yake, bai mai da daidaitakar nan tasa da Allah abar da zai riƙe kankan ce ba, sai ma ya mai da kansa baya matuƙa ta ɗaukar surar bawa, da kuma kasancewa da kamannin ɗan adam... sai ya ƙasƙantar da kansa ta wurin yin biyayya, har wadda ta kai shi ga mutuwa, mutuwar ma ta gicciye. Saboda haka ne kuma Allah ya ɗaukaka shi mafificiyar ɗaukaka, ya kuma yi masa baiwa da sunan nan da yake birbishin kowane suna. (Filibiyawa 2:5-9)*

**Yesu ya bayyana triniti (ɗayantakar mutum uku na Allah) ga almajiransa jim kaɗan kafin a kama shi:**
*"In dai kuna ƙaunata, za ku bi umarnina. Ni ma zan roƙi Uba, zai kuwa ba ku wani Mai Taimako ya kasance tare da ku har abada. Shi ne Ruhu na gaskiya, wanda duniya ba ta iya samunsa, domin ba ta ganinsa, ba ta kuma san shi ba. Ku kam, kun san shi, domin yana zauna tare da kuu, zai kuma kasance a zuciyarku." (Yahaya 14:15-17)*

*"Kowa yake ƙaunata, zai kiyaye maganata, Ubana kuwa zai ƙaunace shi, za mu zo wurinsa mu zauna tare da shi." (Yahaya 14:23)*

*"Duk wannan na faɗa muku ne tun muna tare. Amma Mai Taimako, wato, Ruhu Mai Tsarki, wanda Uba zai aiko cikin sunana, shi ne zai koya muku kome, ya kuma tuna muku duk abin da na faɗa muku." (Yahaya 14:25-26)*

*"Kun dai ji na ce muku zan tafi, in kuma dawo wurinku. Da kuna ƙaunata da kun yi murna saboda za ni wurin Uba, domin kuwa Uban ya fi ni." (Yahaya 14:28)*

*"Amma sa'ad da Mai Taimako ya zo, wanda zan aiko muku daga wurin Uba, wato Ruhu na gaskiya, mai Fitowa daga wurin Uba, shi ne zai shaida ni. Ku ma shaidu ne, domin tun farko kuke tare da ni." (Yahaya 15:26-27)*

*"Duk da haka ina gaya muku gaskiya, zai fiye muku in tafi, domin in ban tafi ba, Mai Taimakon nan ba zai zo gare ku ba. In kuwa na tafi, zan aiko shi gare ku." (Yahaya 16:7)*

*"Daga wurin Uban ne na fito, na shigo duniya, har wa yau kuma zan bar duniya in koma wurin Uba." (Yahaya 16:28)*

*Ba mutumin da ya taɓa ganin Allah daɗai. Makadaicin Ɗa, wanda yake yadda Allah yake, wanda kuma yake a wurin Uba, shi ne ya bayyana shi. (Yahaya 1:18)*

**<u>Domin La'akari:</u>**

Abin lura shi ne lokacin da *Allah* yana magana a cikin Alkur'ani sau da yawa ya fi amfani farkon-mutum-jami'i na ra'ayi (mu), amma sa'ad da Allah yana magana a Littafi Mai Tsarki kusan kullayaumin ya fi amfani da mufuradi (Ni). Har yanzu, bisa ga Littafi Mai Tsarki, Allah ɗayantaka (jam'iyya) ne na mutum uku, yayin da bisa ga Alkur'ani, *Allah* mutum ɗaya ne kadai. Amma don me Allah zai yi amfani da jam'i a ta hanyar yin magana tun da yake shi ɗaya ne kawai kuma ba shi da Da ko kuwa abokin tarayya cikin mulki?

*Babi Na 5*

# Yesu Shi ne Mai Ceton Duniya?

**Alkur'ani ya fada cewa Yesu Annabi ne da kuma Almasihu (Masiha). Duk da haka, ba ta amince da Shi kamar Mai Ceton Duniya ba, sai dai kamar ɗaya cikin Manzanni:**
*Masĩhu ɗan Maryama bai zama ba fãce Manzo ne kawai, haƙĩƙa, manzanni sun shige dage gabãninsa, kuma uwarsa siddika ce. Sun kasance sunã cin abinci. Ka duba yadda Muke bayyana musu ãyõyi. Sa'an nan kuma ka duba yadda ake karkatar da su. (Alkur'ani 5:75)*

*Ka ce: "Mun yi ĩmãni da Allah kuma da abin da aka saukar mana da abin da aka saukar wa Ibrãhĩma da Isma'ĩla da Is'hãƙa da Yãƙũba da jĩkõki, da abin da aka bai wa Mũsã da ĩsã da annabãwa daga Ubangijinsu, bã mu bambantãwa a tsakãnin kõwa daga gare su. Kuma mũ, zuwa gare Shi mãsu sallamãwa ne." (Alkur'ani 3:84)*

**Littafi Mai Tsarki, a wani hannu, ya nuna a nassosi da yawa cewa haƙiƙa Yesu shi ne Mai Ceton Duniya wanda ya mutu kamar Hadaya domin Zunubanmu:**
*Amma tun yana cikin wannan tunani, sai ga wani mala'ikan Ubangiji ya bayyana a gare shi a mafarki, ya ce, "Yusufu ɗan Dawuda, kada ka ji tsoron ɗaukar Maryamu matarka, domin cikin nan nata daga Ruhu Mai Tsarki ne. Za ta haifi ɗa, za ka kuma sa masa suna YESU, domin shi ne zai ceci mutanensa daga zunubansu. (Matiyu 1:21-22)*

*A wannan yankin ƙasa kuwa waɗansu makiyayi suna kwana a filin Allah, suna tsaron garken tumakinsu da dad dare. Sai ga wani mala'ikan Ubangiji tsaya kusa da su, ɗaukakar Ubangiji kuma ta haskaka kewayensu, har suka tsorata gaya, Sai mala'ikan ya ce musu, "Kaɗa ku ji tsoro, ga shi, albishir na kawo muku na farin ciki mai yawa, wanda zai zama na dukan mutane. Domin yau an haifa muku Mai Ceto a birnin Dawuda, wanda yake shi ne Almasihu, Ubangiji. Ga alamar da za ku gani, za ku sami jariri rufe da zanen goyo, kwance a komin dabbobi." (Luka 2:8-12)*

Yesu ya Fada Game da Kansa:
*"...Ɗan Mutum ma ya zo ba domin a bauta masa ba sai dai domin shi ya yi bautar, yǎ kuma ba da ransa fansa saboda mutane da yawa." (Matiyu 20:28)*

**Waɗansu Nassosi sun fada irin wannan:**
*Amma aka yi masa rauni saboda zunubanmu, Aka daddoke shi saboda muguntar da muka aikata. Hukuncin da ya sha ya 'yantar da mu, Dukan da aka yi masa, ya sa muka warke. (Ishaya 53:5)*

*…. Aka tafi da shi domin a kashe shi, Ba wanda ya kula da ƙaddararsa. Aka kashe shi saboda zunubin mutanenmu. (Ishaya 53:8)*

*Bayan shan wahalarsa, zai sāke yin murna... Shi ne bawana, adali, Zai ɗauki hukuncin mutane masu yawa, Ya sa su zama mutanena amintattu. (Ishaya 53:11)*

*Amma shi Almasihu da ya miƙa hadaya guda ta har abada domin kawar da zunubai, sai ya zauna a dama ga Allah. (Ibraniyawa 10:12)*

*Balle fa jinin Almasihu wanda ya miƙa kansa marar aibu ga Allah, ta wurin Madawwamin Ruhu, lalle zai tsarkake lamirinmu daga barin ibada marar tasiri, domin mu bauta wa Allah Rayayye. (Ibraniyawa 9:14)*

*Tun da yake an ƙaddara wa ɗan adam ya mutu sau ɗaya ne, bayan haka kuma sai shari'a, shi Almasihu ma, da aka miƙa shi hadaya sau ɗaya tak,*

*domin ya ɗauke zunuban mutane da yawa, zai sāke bayyana, bayyana ta biyu, ba a kan maganar kawar da zunubi ba, sai dai domin yă ceci waɗanda suke ɗokin zuwansa. (Ibraniyawa 9:27-28)*

*Ku kuma da kuke matattu saboda laifofinku, marasa kaciya ta jiki, Allah ya raya ku tare da Almasihu, ya yafe mana dukkan laifofinmu, ya kuma yanke igiyar nan ta Shari'a da ta ɗaure mu da dokokinta, ya ɗauke ta, ya kafe ta da ƙusa a jikin gicciyensa. (Kolosiyawa 2:13-14)*

*Ya tsamo mu daga mulkin duhu, ya maishe mu ga mulkin ƙaunataccena Ɗansa, wanda ta gare shi ne muka sami fansa, wato, gafarar zunubanmu. (Kolosiyawa 1:13-14)*

*A gare shi dukkan cikar Allah ta tabbata, domin Allah yana farin ciki da haka, da nufin ta wurinsa, Allah yă sulhunta dukkan abubuwa da shi kansa, na ƙasa ko na sama, yana ƙulla zumunci ta wurin jininsa na gicciye. (Kolosiyawa 1:19-20)*

*Ku yi zaman ƙauna kamar yadda Almasihu ya ƙaunace mu, ya kuma ba da kansa dominmu, sadaka mai ƙanshi, hadaya kuma ga Allah. (Afisawa 5:2)*

*Ku yi wa juna kirki, kuna tausayi, kuna yafe wa juna kamar yadda Allah ya yafe muku ta wurin Almasihu. (Afisawa 4:32)*

*Almasihu ya fanso mu daga la'anar nan ta Shari'a, da ya zama abin la'ana saboda mu, domin a rubuce yake cewa, "Duk wanda aka kafa a jikin itace, la'ananne ne." (Galatiyawa 3:13)*

*Wato, Allah ne, ta wurin Almasihu, yake sulhunta 'yan adam da shi kansa, ba ya kuwa lasafta laifofinsu a kansu ba, ...Ku sulhuntu da Allah. Shi da bai san zunubi ba, Allah ya mai da shi zunubi saboda mu, domin mu mu sami adalcin Allah ta wurinsa. (2 Korantiyawa 5:19-21)*

*Mun duba, muna kuma ba da shaida, cewa Uba ya aiko Ɗan ya zama Mai Ceton duniya. (1 Yahaya 4:14)*

*…Ga wanda yake kaunarmu, ya kuma balle mana kangin zunubanmu ta wurin jininsa, ya mai da mu firistoci, mallakar Allah Ubansa… (Wahayin Yahaya 1:5-6)*

*Shi ne duk annabawa suka yi wa shaida, cewa albarkacin sunansa duk mai gaskatawa da shi zai sami gafarar zunubai. (Ayyukan Manzanni 10:43)*

**Yesu ne mabudi ga ceto bisa ga Littafi Mai Tsarki:**
*Saboda ƙaunar da Allah ya yi wa duniya har ya ba da makaɗaicin Ɗansa, domin duk wanda ya gaskata da shi kada ya hallaka, sai dai ya sami rai madawwami. Gama Allah bai aiko Ɗansa duniya domin yă yanke mata hukunci ba, sai dai domin duniya ta sami ceto ta wurinsa. Duk wanda ya gaskata da shi, ba za a yi masa hukunci ba. Wanda kuwa bai ba da gaskiya ba, an riga an yi masa hukunci, domin bai gaskata da sunan makaɗaicin Ɗan Allah ba. (Yahaya 3:16-18)*

*Gama ba na jin kunyar bishara, domin ita ce ikon Allah mai kai kowane mai ba da gaskiya ga samun ceto, Yahudawa da fari, sa'an nan kuma al'ummai. (Romawa 1:16)*

*Amma kuwa Allah yana tabbatar mana da ƙaunar da yake yi mana, wato tun muna masu zunubi, Almasihu ya mutu dominmu. To, tun da yake a yanzu an kuɓutar da mu ta wurin jininsa, ashe kuwa, ta wurinsa za mu fi samun kārewa daga fushin Allah ke nan. In kuwa tun muna maƙiyan Allah aka sulhunta mu da shi ta mutuwar Ɗansa, to, da yake an sulhunta mu, ashe kuwa, za a fi kāre mu ta wurin rayuwarsa ke nan. (Romawa 5:8-10)*

*…In kai da bakinka ka bayyana yarda, cewa Yesu Ubangiji ne, ka kuma gaskata a zuciyarka Allah ya tashe shi daga matattu, za ka sami ceto. (Romawa 10:9)*

*Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyan nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto." (Ayyukan Manzanni 4:12)*

*Babi Na 6:*

# Yesu Shi ne Matsakanci Tsakanin Allah da 'Yan Adam?

**Littafi Mai Tsarki da Alkur'ani duk sun bayyana cewa Allah Mai Tsarki ne, Mahaliccin dukan abubuwa, Maɗaukaki, Masanin duka, Ya Kasance ko'ina da kuma Madawwami, kuma ba wanda ya iya kusantan Allah ta wurin cancantar kansu.**

**Alkur'ani ya fada** cewa zai yiwu mutum ya yi godo ga Allah tare da izininsa kadai:

*Allah, bãbu wani Ubangiji fãce Shi, Rãyayye, Mai tsayuwa da kõme, gyangyaɗi bã ya kãma Shi, kuma barci bã ya kãma Shi, Shi ne da abin da yake a cikin sammai da abin da yake a cikin ƙasa. Wane ne wanda yake yin cẽto a wurinSa, fãce da izninSa? Yana sanin abin da yake a gaba gare su da abin da yake a bãyansu. Kuma bã su kẽwayẽwa da kõme daga ilminSa, fãce da abin da Ya so... (Alkur'ani 2:255)*

**Bisa ga Littattafai, duk kome ya canza ta wurin zuwan Yesu:**
Wannan ya tabbata a kan mutuwar Yesu lokacin da labulen haiƙali, mai raba wuri mafi Tsarki daga wani sashi na haiƙalin, aka raba shi daga bisa zuwa kasa ta wurin ikon allahntaka, kamar alama ce budewar hanya zuwa ga Allah ta wurin mutuwar Yesu. A sakamakon haka, da karfin hali za mu iya kusaci kursiyin Allah ta wurin Yesu kamar yadda an iya karanta a cikin *Ibraniyawa 10:19-22* da kuma *Ibraniyawa 4:14-16.*

**Kowane littafi na Littafi Mai Tsarki ya nuna, a wasu hanya, ga Almasihu (Masiha) da aka alkawarta:**
Sura goma sha biyu na Fitowa ya kunshi bayyanin ragon Idin Ketarewa wanda jininsa ya ceci Isra'ilawa daga mutuwa lokacin da suka tsira daga bauta a Masar. Wajibi ragon ya zama na miji, mara aibu da kuma babu karya kashi, wanda ya zama Kwatancin Almasihu (Masiha) kamar ragon hadaya.

Yahaya Mai Baftisma ya sami wahayin wannan lokacin da ya ga Yesu:
*Kashegari Yahaya ya tsinkayo Yesu na nufo shi, sai ya ce, "Kun ga ga Ɗan Rago na Allah, wanda zai ɗauke zunubin duniya!" (Yahaya 1:29)*

Bitrus ya nuna ra'ayi:
*Domin kun sani an fanshe ku ne daga al'adunku na banza da wofi da kuka gāda, ba da abubuwa masu lalacewa kamar azurfa da zinariya ba, sai dai da jinin nan mai daraja na Almasihu, kamar na ɗan rago marar naƙasa, marar tabo. (1 Bitrus 1:18-19)*

Almajiri Yahaya ya sami wahayi na Sama inda ya ga Yesu kamar ɗan Rago na Allah (*dubi Wahayin Yahaya 5:6-14; 7:9-17; 22:1-3)*

**Duka Alkur'ani da Littafi Mai Tsarki sun yi jawabi akan damuwar zunubi na 'yan Adam amma bambancin shi ne ko an magance ta a cikin Yesu ko babu –** ko Yesu shi ne wanda ya yi ikirari yake ko kuwa an gicciye shi domin cetonmu kamar yadda annabawa suka yi annabci da kuma yadda mabiyansa suka yi iƙirari sun shaida.

Kamar yadda aka furta a cikin Alkur'ani:
*Wancan ne Ĩsã ɗan Maryamu, maganar gaskiya wadda suke shakka a cikinta. (Alkur'ani 19:34)*

**Littafi Mai Tsarki ya bayyana cewa Yesu shi ne matsakanci kadai tsakanin Allah da 'yan Adam; cewa ba wanda yake da dama zuwa wurin Allah ko ya shiga Sama ba tare da Yesu ba:**
*Yesu ya ce masa, "… Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina." (Yahaya 14:6)*

*Saboda haka, yana da ikon ceton masu kusatowa ga Allah ta wurinsa, matuƙar ceto, tun da yake kullum a raye yake saboda yi musu addu'a... Wannan ya yi ta ne sau ɗaya tak, lokacin da ya miƙa kansa hadaya. (Ibraniyawa 7:25, 27)*

*Saboda haka, shi ne matsakancin sabon alkawari, domin waɗanda aka kira su karɓi dawwamammen gādon da aka yi musu alkawari, tun da yake an yi wata mutuwa mai fansar waɗanda suke keta umarni a game da alkawarin farko. (Ibraniyawa 9:15)*

*Amma duk iyakar waɗanda suka karɓe shi, wato, masu gaskatawa da sunansa, ya ba su ikon zama 'ya'yan Allah. (Yahaya 1:12)*

Shawulu daga Tarsus ya tsananta wa Kirista da kwazo har sai ran da Yesu ya tsayar da shi a hanyarsa zuwa Dimashku inda ya yi niyyar ya ɗaure cikin kurkuku duk Kirista da ya samu ya kuma kawo su kamamu zuwa Urushalima. Wannan tafiya, wanda za a iya karanta shi a *Ayyukan Manzanni 9:1-19,* da ban mamaki ya canja rayuwar Shawulu har ya zama mabiyin Almasihu da kishi:
*Yana tafiya ke nan, ya yi kusa da Dimashƙu, ba zato sai ga wani haske daga sama ya haskaka kewaye da shi. Sai ya fāɗi, ya kuma ji wata murya tana ce masa, "Shawulu, Shawulu, don me kake tsananta mini?" Shi kuma ya ce, "Wane ne kai, ya Ubangiji?" Sai ya ce, "Ni ne Yesu wanda kake tsananta wa.…" (Ayyukan Manzanni 9:3-5)*

Wannan mutumin, Shawulu, daga baya an fi saninsa da Manzo Bulus, ya rubuta wasiku da dama na Sabon Alkawari. Bari mu tsinkayo kaɗan daga rubuce-rubucensa:
*Maganar nan tabbatacciya ce, ta kuma cancanci a karɓe ta ɗungum cewa, "Almasihu Yesu ya shigo duniya ne domin ceton masu zunubi," ni ne kuwa babbansu. (1 Timoti 1:15)*

*Wannan kyakkyawan abu ne, kuma abin karɓa ne a gun Allah Mai Cetonmu, wanda yake son dukkan mutane su sami ceto, su kuma kai ga sanin gaskiya. Domin Allah ɗaya ne, matsakanci kuma ɗaya ne, a tsakanin Allah da*

*mutane, Almasihu Yesu, mutum, wanda ya ba da kansa fansa saboda kowa da kowa. An kuwa yi shaidar wannan a daidai lokacinsa. (1 Timoti 2:3-6)*

*Ta gare shi ne muka sami fansa albarkacin jininsa, wato yafewar laifofinmu… (Afisawa 1:7)*

Bisa ga Littafi Mai Tsarki, dukkan mutane sun yi zunubi kuma ya kamata a tsarkake zunubanmu a kuma gafarta mana domin mu sami shigan Sama:
*...gama 'yan adam duka sun yi zunubi, sun kasa kuma ga ɗaukakar Allah. Amma ta wurin alherin da Allah ya yi musu kyauta, sun sami kuɓuta ta wurin fansar da Almasihu Yesu ya yi. Allah kuwa ya ayyana Yesu Almasihu ya zama hadayar sulhu, ta wurin ba da gaskiya ga jininsa. Allah kuwa ya yi haka domin ya nuna adalcinsa ne, domin dā saboda haƙurinsa ya jingine zunuban da aka gabatar... (Romawa 3:23-25)*

*Gama sakamakon zunubi mutuwa ne, amma baiwar Allah ita ce rai madawwami a cikin Almasihu Yesu Ubangijinmu. (Romawa 6:23)*

**Domin La'akari:**
Duka Alkur'ani da Littafi Mai Tsarki suna koyar cewa 'yan Adam suna da dawwamammen ruhu, kuma za su fuskanci Ranar Kiyama inda Allah zai kayyade Aljanna (Firdausi)/Sama ko kuwa Jahannama (Gidan Wuta), ƙarshen makomansu ke nan.

Bisa ga dukan Alkur'ani da Littafi Mai Tsarki, aikata ayyukan kirki yana da muhimmanci. Duk da haka, bisa ga Littafi Mai Tsarki, ayyukan kirkinmu kadai ba su isa su samo mamu shigan Sama ba, domin ba za su iya tsarkake zunubanmu ba. *(dubi Ibraniyawa 9:22)*

Littafi Mai Tsarki ya faɗa cewa daga kauna tsantsa, Allah ya aiko tilon Ɗansa Yesu (Isa) cikin wannan duniya domin mu sami rai madawwami tare da Allah. Ba tare da karban Yesu a matsayin Ubangijinmu da Mai Cetonmu ba, za mu bace na har abada. *(dubi Yahaya 3:16)*

**Shi ya sa tambayar nan wane ne Yesu, yana da muhimmanci kwarai.**

*Babi Na 7*

# Tabbaci Na Tushen Rubutu

Ko da shi ke Alkur'ani da kuma Littafi Mai Tsarki suna da amincewa a kan ababa da yawa, sun nuna bambancin ra'ayi a kan waɗansu muhimman al'amura. Wannan ya kai ga tambaya na gaggawa mai kalubale kuma: **Mene ne gaskiya?**

Babban darasi wanda Alkur'ani da Littafi Mai Tsarki suka saba wa juna shi ne ko Yesu shi ne Ɗan Allah da kuma ko ya mutu a bisan gicciye. Waɗannan su ne muhimman tambayoyi.

Domin a rungume gaskiya yana bukata a zama da budadiyar hankali da zuciya, a zama a shirye domin bincika don a sami gaskiya a kuma yarda da ta da zarar an samo ta. **Tambayar yana da muhimmanci: Mene ne ainihin gaskiya game da Yesu?** Muna a shirye mu dauke dama mu samo ta, domin bisa ga amsa rayuwarmu zai iya canjawa har abada?

**<u>Amincewar Alkur'ani da Littafi Mai Tsarki:</u>**

Bari mu kamanta su tushen:

**Alkur'ani** ta zo ga kasancewa ta wurin Annabi Muhammadu wanda ya karba sakonta daga mala'ika.

Annabawa, sarakuna, alkalai, almajiran Yesu, ‘yan’uwansa biyu, likita na kiwon lafiya, da waɗansu mutane masu tsoron-Allah ne suka rubuta **Littafi Mai Tsarki.** Allah ya yi tafiya tare da su ya kuma yi magana kai tsaye ga waɗansunsu kuma mala’iku sun ziyarci yawancinsu. Dukansu Ruhun Allah ne ya hurarre su. *(dubi 2 Timoti 3:16)*

Waɗansu suka rubuta abin da sun shaida, labaran abin da ya faru a idonsu. Waɗansu sun rubuta sakonni daga Ubangiji, wakokin addu’a da sujada, kalmomin hikima, annabce-annabce da wahayi daga Ubangiji.

**Taburin Kamantawa da Amincewa:**

| **Batu na Kamantawa** | **Littafi Mai Tsarki** | **Alkur’ani** |
|---|---|---|
| Yesu – Ɗan Allah | I | A’a |
| Yesu – ya mutu a bisa gicciye | I | A’a |
| Rubutaccen annabce-annabce game da Almasihu (Masiha) | Sama da annabce-annabce 300 game da Almasihu (Masiha) wanda za a iya samu cikin Littafi Mai Tsarki, rubutaccen karni da yawa kafin haifuwar Yesu. | |

| | | |
|---|---|---|
| Sakonni daga mala'iku game da wane ne Yesu | Mala'ika ya bayyana ga Maryamu ya yi shela cewa za ta haifi da wanda za a kira shi Ɗan Madaukaki, Ɗan Allah. *(dubi Luka 1:30-35)*<br>Mala'ika ya bayyana ga Yusufu ya yi shela cewa Maryamu za ta haifi da wanda zai ceci mutanensa daga zunubi. *(dubi Matiyu 1:20-21)*<br>Mala'ika ya bayyana ga makiyaya a fili kusa da Baitalami, ya yi masu shelar bishara cewa an haifi Mai Ceto wanda shi ne Almasihu (Masiha), Ubangiji. *(dubi Luka 2:8-11)* | Mala'ika ya bayyana ga Maryamu, ya yi shelar cewa za ta haifi, za a kira shi Almasihu/ Masiha. *(dubi Alkur'ani 3:45)*<br>Mala'ika ya bayyana ga Annabi Muhammadu, ya yi shela cewa Yesu ba ɗan Allah ba ne. *(dubi Alkur'ani 4:171; 6:101; 9:30)* |
| Shaidu da yawa sun shaida cewa Yesu ne Ɗan Allah | Yahaya Mai Baftisma da almajiran Yesu:<br>Bitrus, Yakubu da Yahaya – dukansu hudu sun ji murya daga Sama yana bayyana cewa Yesu ne Ɗan Allah kuma almajirai ukun sun ga Yesu yadda ya sake kamaninsa na ɗaukaka *(dubi Matiyu 3:13-17; Luka 9:28-35)* | |

| | | |
|---|---|---|
| An gicciye shaidun Yesu | A Tsaye kusa da Gicciye:<br>Almajiri Yahaya, Maryamu uwar Yesu, yar'uwar mahaifiyarsa, Maryamu matar Kilofas da kuma Maryamu Magadaliya *(dubi Yahaya 19:25)*<br>Duba wa daga nesa:<br>Mutane da yawa da sun san Yesu, da duk matan da suka biyo shi tun daga Galili *(dubi Luka 23:49)* | |
| Shaidu sun ba da shaida cewa Yesu ya tashi daga matattu | Mala'iku biyu sun bayyana ga mata waɗanda sun je da niyyar shafe jikin Yesu sun kuma gaya masu cewa Ya tashi daga matattu. *(dubi Luka 24:1-8)*<br>Maryamu Magadaliya, duk almajiransa, Shawulu daga Tarsus da waɗansu da yawa sun sadu da Yesu bayan tashinsa daga matatu. *(dubi Yahaya 20:10-31; Ayyukan Manzanni 9:3-7; 1 Korantiyawa 15:6-7)* | |

| | | |
|---|---|---|
| Likkafanin Turin | An gaskata cewa Likkafanin Turin shi ne kyalle na bison Yesu da an adana, wanda dukan Linjila (Bishara) hudu na Littafi Mai Tsarki sun ambata. | |
| <u>Lokaci:</u><br>Daga ranar aukuwa zuwa ranar rubuta takardun | An gaskata cewa an rubuta Sabon Alkawari a tsakanin shekaru 40 da 100 AD. * An rubuta Linjila (Bishara) hudu tsakanin 60 da 95 AD, suna ɗauke da labarin Yesu wanda shaidu dabam-dabam suka fada. An ba da labarin gicciye da tashin Yesu daga matattu a cikinsu filla-filla. An rubuta Bisharar Markus kusan shekaru 30 bayan an gicciye Yesu, yayin da an rubuta Wasikar farko na Manzo Bulus kusan shekara 50 AD, kimanin shekaru 20 bayan mutuwar Yesu. Wannan ɗan matsattsen lokaci ya goyi bayan gaskiyar takardun aukuwar nan da karfi. | An rubuta Alkur'ani tsakanin shekaru 610 da 632 AD, kusa da shekaru 600 bayan tafiyar Yesu a duniya. |

| | | |
|---|---|---|
| Adana Rubutu ta Asali | An kimanta lokacin adana rubutun farko na Sabon Alkawari a shekara ta 130 AD. Sama da 24,000 na rubutun Sabon Alkawari yana wanzuwa har wa yau waɗanda suke a cikin fihirisa, ta haka aka tabbatar cewa an adana asalin rubutun Sabon Alkawari ba tare da an canja ma'anarta ba. | Adana rubutun farko na Alkur'ani yana kusa a lokaci sa'ad da an yi rubutun ainihi, wanda ya nuna cewa an adana asalin rubutun Alkur'ani babu canja ma'anarta. |
| Littattafan Mataccen Teku 8) wanda an samu a shekara ta 1946, 1947 da 1956 | Littattafan na Mataccen Teku rubutu ne da ya kunshi sassan dukan littattafai na Tsohon Alkawari, banda Littattafan Nehemiya da Esta, duk da na Ishaya (a 734 cm a tsayi). Wadannan rubutu, wanda suke kusan shekaru 2000 a tsufa, sun yi daidai sarai da wasu rubutu da sun kasance, yana tabbatar cewa an adana Littafi Mai Tsarki ba tare da an canja ma'anarsa ba a dukan lokaci. | |

| | | |
|---|---|---|
| Babu Kuskure a Rubutun | Littafi Mai Tsarki ya tabbatar da shi da kuskure ta wurin cikar annabce-annabce masu yawa da ilmin kimiya na kayan tarihi da binciken masu ilmin tarihi da sun yi daidai da aukuwar, mulki, adadi, yake-yake, hanyoyin rayuwa da jerin lokuta da an samo cikin Littafi Mai Tsarki. | |

* AD (Anno Domini – Bayan Haifuwar Almasihu)

# Rufewa

Bari mu rufe da kwatanta da furucin da Alkur'ani ya shaida:
*Ka ce: "Idan har akwai dã ga Mai rahama, to, nĩ ne farkon mãsu bauta (wa ɗan)." (Alkur'ani 43:81)*

Wannan shaidar ta gaskiya ce kwari, domin idan mun ga Yesu a matsayin Ɗan Allah, za mu kuwa ga ya cancanci sujadarmu.

Yesu ya ce:
*"Ku zo gare ne dukanku masu wahala, masu fama da kaya, ni kuwa zan hutasshe ku." (Matiyu 11:28)*

*"…Ga shi, ni kuma kullum ina tare da ku har ya zuwa matukar zamani." (Matiyu 28:20)*

**Bisa ga Alkur'ani da Littafi Mai Tsarki, za mu amince da kalmomin Yesu:**
*Wancan ne Isa ɗan Maryamu, maganar gaskiya… (Alkur'ani 19:34)*

*Yesu ya amsa, "… Domin haka musamman aka haife ni, don haka kuma musamman na shigo duniya, domin in shaidi gaskiya. Kowane mai mai kaunar gaskiya kuwa yakan saurari muryata." (Yahaya 18:37)*

Idan kai, mai karatu, ka karanta wannan takarda a hankali, na gaskata ka sani a yanzu a zuciyarka wane ne Yesu da kuma abin da ke gaskiya a gare ka.

Domin karin bayyani a kan mutumin nan Yesu mai al'ajibi, za ka iya karanta Linjila/Bishara (Labari Mai Dadi) a cikin Sabon Alkawari na Littafi Mai Tsarki waɗanda ya kunshi cikakken labaran Yesu waɗanda Kirista, da wasu Musulmi, suke koma ga.

# Sunayen Yesu a cikin Alkur'ani da kuma Littafi Mai Tsarki

<u>Cikin Alkur'ani:</u>
Isa/Yesu *(Alkur'ani 3:45)*
Almasihu (Masiha) *(Alkur'ani 3:45)*
Ɗan Maryamu *(Alkur'ani 19:34)*
Kalman Gaskiya *(Alkur'ani 19:34)*

<u>Cikin Littafi Mai Tsarki:</u>
Immanuwel *(Ishaya 7:14)*
Yesu Almasihu (Yeshuwa, Masiha) *(Ayyukan Manzanni 4:10)*
Yesu Banazare *(Luka 24:19)*
Yaron kafinta *(Matiyu 13:55)*
Ɗan Mutum *(Matiyu 25:31)*
Ɗan Allah *(Markus 3:11)*
Sarkin Yahudawa *(Matiyu 27:37)*
Mahawarci Mai Al'ajibi *(Ishaya 9:6)*
Allah Maɗaukaki *(Ishaya 9:6)*
Uba Madawwami *(Ishaya 9:6)*
Sarkin Salama *(Ishaya 9:6)*
Ɗan Ragon Allah *(Yahaya 1:29)*
Zaki na kabilar Yahuda *(Wahayin Yahaya 5:5)*
Amintace, Mai Gaskiya *(Wahayin Yahaya 19:11)*
Kalman Allah *(Wahayin Yahaya 19:13)*
Ubangiji Yesu Almasihu *(Kolosiyawa 1:3)*
SARKIN SARAKUNA, UBANGIJIN IYAYENGIJI *(Wahayin Yahaya 19:16)*

# Kima daga Koyarwar Yesu

*Kuma Ina warkar da wanda aka haifa makaho da kuturu, kuma ina rayar da matattu… (Alkur'ani 3:49)*

*Domin ku zama 'ya'yan Ubanku wanda yake cikin Sama. Domin yakan sa rana tasa ta fito kan mugaye da kuma nagargaru, ya kuma sako ruwan sama ga masu adalci da marasa adalci. (Matiyu 5:44)*

*Saboda haka duk abin da kuke so mutane su yi muku, ku ma sai ku yi musu, domin wannan shi ne Attaura da koyarwar annabawa. (Matiyu 7:12)*

*Saboda haka sai ku yi addu'a kamar haka:*
*Ya Ubanmu, wanda yake cikin Sama,*
*A kiyayye sunanka da tsarki.*
*Mulkinka yă zo,*
*A aikata nufinka a duniya kamar yadda ake yi a Sama.*
*Ka ba mu abincinmu na yau.*
*Ka gafarta mana laifofinmu,*
*Kamar yadda mu ma muke gafarta wa wadanda suke yi mana laifi.*
*Kada ka kai mu wurin jaraba,*
*Amma ka cece mu daga Mugun.*
*Domin mulki, da iko da daukaka naka ne har abada. Amin. (Matiyu 6:9-13)*

*1)* Lucian of Samosata. (165). *The Passing of Peregrinus (The Death of Peregrinus).* (11-13). English Translation: A.M. Harmon. (1936). (Vol. 5, p.12-15). Loeb Classical Library edition.
https://earlychurchtexts.com/public/lucian_passing_of_peregrinus.htm

*2) The Babylonian Talmud.* (70-200). English Translation: I. Epstein. (London: Soncino, 1935). Vol. III, Sanhedrin 43a, 281, cited in Habermas. The Historical Jesus, 203.
https://www.bethinking.org/jesus/ancient-evidence-for-jesus-from-non-christian-sources

*3)* Josephus, Flavius. (93). *Antiquities of the Jews (Book 18,* chapter 3.3) English Translation: William Whiston. (1737)
https://archive.org/details/completeworksofj03jose/page/94/mode/2up

*4)* Pliny the Younger. (112). *Epistulae X.96* English Translation: William Whiston.
www.pbs.org/wgbh/pages/frontline/shows/religion/maps/primary/pliny.html

*5)* Tacitus, Cornelius. (116). *Annals (Book 15,* chapter 44) Edited for Perseus, New York by Church, Alfred John and Brodribb, William Jackson. Reprinted 1942. Random House Inc.
http://www.perseus.tufts.edu/hopper/text?doc=Tac.+Ann.+15.44&fromdoc=Perseus%3Atext%3A1999.02.0078

*6)* Good Shepherd Film Production. (2016). Part 2 *Science Explains Shroud Image* NEW 2016 Video [Video]. Youtube.
https://www.youtube.com/watch?v=efEDb2jHyMY


*7)* Reel Truth History Documentaries. (2019, 11. Sept.). *Turin Shroud: The New Evidence (Shroud of Turin) History Documentary Reel Truth History* [Video]. Youtube.
https://www.youtube.com/watch?v=NVovTvDjjCg

*8) The Israel Museum, Jerusalem.* The Dead Sea Scrolls. Obtained on February 12, 2021 from:
https://www.imj.org.il/en/wings/shrine-book/dead-sea-scrolls

WANE NE YESU? Wannan littafi yana kokarin nuna haske a kan muhimman tambaya ta yin tunani a kan wasu muhimman darasi dangane da Yesu, wanda Musulmi da Kirista suke gani dabam-dabam:

- Yesu ya Mutu a Bisan Gicciye?
- Yesu Shi Ne Dan Allah?
- Yesu da Kansa Allah ne?
- Yesu Shi Ne Mai Ceton Duniya?
- Yesu Shi ne Matsakanci Tsakanin Allah da 'Yan Adam?

Wane amsoshi ne Alkur'ani, Littafi Mai Tsarki, masu ilmin tarihi da kuma Yesu kansa sun bayar ga wadannan tambayoyi? Duk da kankantarta, wannan littafi ya tabi matsanancin batutuwa masu nauyi. Yan bincika su tushe daban-daban da kuma kamanta amsoshin da an samu domin a bayyana wane ne Yesu yake da gaske.



**"A lokacin da duk aka ce kuma an yi sa'annan rayuwarmu a duniya ta kare, za a bayyana tambaya mafi muhimmanci: "Mene ne ka yi game da Yesu Almasihu?" Ka gaskata da shi annabi ne? Mai adadin tarihi ne? Wani da ya rika zagawa na aikin alherin? Mahaukaci ne? Ko kuwa Shi Mutumin da Ya ce Shi ne, Da wanda Uban na cikin Sama ya aika, cikakken Allah, cikakken mutum, Yesu Mai Ceton duniya? Gunna Magga Palsdottir ya yi rubucen malamai, aikin fasaha a kan ainihi wane ne Yesu Almasihu. Ba za ka so rasa karatun wannan littafi ba domin babban karatu kawai ba, amma wanda a zahiri rayuwarka ya dogara ga gaskiyar da ke cikin wannan aikin."**

**- Patricia Bootsma.**

*Mataimakiyar Shugaba na,*
*Catch the Fire North, South and Central America.*
*Marubuci: Convergence, Raising Burning Hearts,*
*A Lifestyle of Divine Encounters.*
*Mai Maganar Jadawalin Ziyarar ta da Shugaban Gidan Addu'a.*

ISBN 978-9935-526-11-3